NAZARIN HAUSAR KAN TITI

NA

Abdulqadir ABUBAKAR ZAILANI
MA/ARTS/7223/2009-2010

BINCIKEN DA AKA GUDANAR DOMIN NEMAN DIGIRI NA BIYU (Hausa) A SASHEN NAZARIN HARSUNA DA AL'ADUN AFIRKA, JAMI'AR AHMADU BELLO, ZARIYA.

NIJERIYA.

MAYU, 2013

NAZARIN HAUSAR KAN TITI

BY

Abdulqadir ABUBAKAR ZAILANI
MA/ARTS/7223/2009-2010

A THESIS SUBMITTED TO THE POSTGRADUATE SCHOOL
AHMADU BELLO UNIVERSITY, ZARIA.
NIGERIA.

IN PARTIAL FULFILMENT FOR THE AWARD OF DEGREE OF MASTER ARTS IN AFRICAN LANGUAGES (HAUSA).

DEPARTMENT OF AFRICAN LANGUAGES AND CULTURES
AHMADU BELLO UNIVERSITY, ZARIA.
NIGERIA

MAY, 2013

DECLARATION

I declare that the work entitled " Nazarin Hausar Kan Titi" has been performed by me in the Department of African Languages and Cultures, under the supervision of Dr. B.S.Y. Al-Hassan and Dr. M.T. Yakawada. The information derived from the literature has been duly acknowledged in the text and a list of references provided. No part of this thesis was previously presented for another degree or diploma at any University.

Abdulqadir, ABUBAKAR ZAILANI ---------- ----------
Signature Date

CERTIFICATION.

This project entitled " **Nazarin Hausar Kan Titi**" by Abdulqadir Abubakar Zailani, meets the regulations governing the award of the degree of Master of Arts, African Languages (Hausa) of Ahmadu Bello University, Zaria, and is approved for its contribution to knowledge and literary presentation.

---------- Date: ----------
Dr. B. S. Y. AL-Hassan

Major Supervisor.

---------- Date: ----------
Dr. M. T. Yakawada

Minor Supervisor.

---------- Date: ----------
Dr. B. Abdullahi

Head of Department .

---------- Date: ----------
Prof. A. A. Joshua

Dean, PG School.

DEDICATION

I have dedicated this research work to my late grandfather Malam Zailani Isah, may his soul rest in peace and my elder brother Malam Mustapha Abubakar.

GODIYA

Dukkan godiya da yabo sun tabbata ga Allah, Ubangijin Sammai da Qassai da duk abubuwan da ke tsakaninsu. Mai yin yadda Ya so, a lokacin da Ya so. Tsira da amincin Allah su tabbata ga fiyayyen halitta Annabi Muhammad (S.A.W), Ina mai yin salati marar adadi ga Annabi da alayansa da sahabbansa da kuma waxanda suka bi tafarkinsa har zuwa ranar qiyama.

Bayan haka, ina miqa godiya ta musamman ga malamaina kuma jagororin wannan aiki Dakta B.S.Y. Al-Hassan da Dakta. M T. Yakawada saboda xora ni da suka yi a kan hanya ta fuskar shawarwari da gyare-gyare masu amfani da ma'ana waxanda suka taimaka wajen kammaluwar wannan kundin bincike. Na gode, Allah Ya sa a gama lafiya. Ina mai matuqar godiya ga mahaifana da mai xakina (SM) da 'ya 'yana Ummu-Kulsum da Abdulrahman da kuma Hafsa. Ban manta da yaya babba ba Mal. Mustapha da dukkanin iyalan Alhaji Abubakar S. Zailani, Allah Ya albarkace mu baki xaya.

Haka kuma ina mai godiya ga malamaina waxanda suka shayar da ni ilimi a matakai daban-daban. Daga cikinsu akwai Farfesa Xalhatu Muhammad da Farfesa Munir Mamman da Farfesa Mu'azu Sani Zariya da Farfesa M. A. Umar da Dakta ML Amin da Dakta B. Abdullahi da Dakta S A Kargi da Dakta Aliyu Bussa da Mal. M R Tahir da sauransu. Duk cikansu a fagen Digiri na Biyu. Ban manta da Dakta Ramlatu ba, na gode Allah Ya sa a gama lafiya.

Ina mai godiya ga Farfesa A. H. Amfani da Farfesa Salisu A. Yakasai da Farfesa Ibrahim A. Malumfashi da Farfesa M. A. Dantumbishi dukkaninsu da ke Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya Jami'ar Usmanu Xanfodiyo da ke Sakkwato.

Ban manta da abokanan karatuna ba a fagen digiri na biyu, kamar Abubakar Ayuba da Hassan Rabeh da Maikuxi Umar (Cash Man) da Rabi'u Bashir da Musa Tela da Xalladi Shu'aibu da Suleiman Adamu Ladan da Magaji Yahaya da kuma Safiya Muhammed. Ina mai roqon mai duka da ya ci-gaba da shiryar da mu kan hanya madaidaiciya, Ya kuma tsare mu daga sharrin masu sharri.

A qarshe, ina godiya ga Suleiman Ibrahim BT da Mustapha Muhammad Umar (Almu Getso) na UDUS Sakkwato da Adamu Usman da Lukman M. Amin da ma dukkanin waxanda suka taimake ni wajen gudanar da wannan aiki ta kowace irin hanya. Allah Ya albarkaci zuriya.

Alhamdulillah.

Abdulqadir ABUBAKAR ZAILANI

MA/ARTS/7223/2009-2010

ABSTRACT

This research entitled “Nazarin Hausar Kan Titi” studies the varieties of Hausa spoken by different groups of Hausa people in their daily activities. Street language or Slang is just an euphemism (kinaya) used to describe a language or a dialect used in the cause of communication by socio-lect with the intention of hiding some vital information, deceiving or to carry away the minds of those who do not belong to their folks, so that the meaning will be distorted and can only be understood by them or those explained to. Socio-lect in Hausa contributed immensely in enriching the language as a result of borrowing or coining of new words and meaning from old ones. The research, studies the kind of language expression or words and phrases they use in communication which are informal. The groups studied are the transit that include bus drivers, conductors and motor cycle riders. The drinkers or intoxicators are not left out in the study, those who take alcohol, hard drugs that consist of Indian hemp, solution, hard drugs and codeine syrup are among the groups studied. The work discover that syntactically the sentences they used have no Noun Phrase (NP), its normally Verbal Phrase (VP) and the Verbal Grade they normally used are grade 1, 2, 4 and 6 and they also they used simple sentence.

TSAKURE

Hausar kan Titi, kinaya ce da aka yi amfani da kalmar titi don bayyana wani nau'i na Hausa da ake amfani da shi da manufar bayyana karin harshen rukuni da wasu mutane ke yi don sadarwa. Ana iya samun wannan nau'i na Hausa a ko'ina, ba fa ana nufin Hausar mutanen banza ne ba. Akan yi wannan nau'i na Hausa ne da niyyar voye wani ko wasu muhimman saqwanni da suka danganci harkokin rayuwarsu na yau da kullum, don a vad da bami ko a cuci ko a yaudari mutum wanda wannan rukuni na mutane ko majiya harshe xaya ke yi; ta yadda sai xan hannu ne kawai kan gane ko ya fahimci ma'anar abin da ake faxa ko ake nufi. Wannan nau'i na Hausa da rukunin Hausawa ke yi na taimakawa wajen bunqasa harshen Hausa, hakan ya haifar da sabbin ma'anoni daga tsofaffin da aka sani da kuma qirqirar wasu sababbin kalmomi a harshen. Binciken ya nazarci wannan nau'i na Hausa ne domin nuna yadda Hausar yau da kullum ta haifar da qirqira da aro da ke xauke da kinaya a karin harshen da ya kevanta da rukunin masu motocin haya da 'Yan babura, wato 'Yan a-cava da kuma mashaya. Mashayan da aka nazarci Hausarsu su ne: 'Yan giya da 'Yan wiwi da 'Yan qwaya da 'Yan shava da kuma 'Yan kodin ko zumar kemis. Binciken ya gano cewa jimlolin da suke amfani da su a lokacin sadarwa sauqaqa ne domin zubi da tsarin mafi yawan su ba su da yankin suna sai yankin aiki kawai. Sannan ta vangaren azuzuwan kalmomin nahawu sun fi amfani da wakilin suna da aikatau da kuma bayanau, duk da yake a kan sami sauran azuzuwan kalmomin Hausa na nahawu kuma sun fi amfani da aikatau 'Yan aji 1 da 2 da 4 da kuma aji 6. Harshen Hausa na bunqasa sakamakon qirqira da aro da fassarar sababbin kalmomi da ma jimloli da ake samu, kuma ma'anarsu ta kevanta ne da wuri ko yanayin da ake ciki a lokacin sadarwar.

QUNSHIYA

Shafin Tabbatarwa. ----------

Shafin Amincewa. ----------

Shafin Sadaukarwa. ----------

Shafin Godiya. ----------

Tsakure. ----------

Babi Na Xaya: Gabatarwa

1.1 Shimfixa ---------- 1

1.2 Dalilan Bincike ---------- 6

1.3 Manufar Bincike ---------- 7

1.4 Tambayoyin Bincike ---------- 8

1.5 Matsalolin Bincike ---------- 9

1.6 Muhimmancin Bincike ---------- 10

1.7 Hasashen Bincike _---------- 11

1.8 Hanyoyin Gudanar da Bincike ---------- 11

1.9 Farfajiyar Bincike ---------- 12

1.10 Ma’anar Wasu Kalmomi ---------- 13

1.10.1 Sulo ---------- 13

1.10.2 Kodin ---------- 13

1.10.3 Zumar kemis ---------- 13

1.10.4 Shava ---------- 13

1.10.5 Qwaya/Qwayoyi ---------- 13

1.10.6 Maye ---------- 14

1.10.7 Shaye-Shaye ---------- 14

1.11 Naxewa. ---------- 14

Babi Na Biyu: Waiwayen Ayyukan da suka Gabata

2.1 Gabatarwa ---------- 15

2.2 Waiwayen Ayyuka a kan Hausar Rukuni ---------- 15

2.2.1 Litattafa ---------- 15

2.2.2 Kundayen Bincike ---------- 19

2.2.3 Muqalai ---------- 27

2.3 Naxewa. ---------- 35

Babi Na Uku: Mutanen Kan Titi da Sana'o'insu

3.1 Gabatarwa ---------- 36

3.2 Karin Harshe ---------- 36

3.2.1 Majiya Harshe Xaya ---------- 40

3.3 Dangantakar Harshe da Al'umma ---------- 41

3.4 Ma'anar Kan Titi ---------- 47

3.4.1 Rayuwar Kan Titi ---------- 48

3.4.2 Mutanen Kan Titi ---------- 48

3.5 Sana'o'in Kan Titi ---------- 51

3.5.1 Masu Motocin Haya ---------- 52

3.5.1.1 Yan Bas (Bus) ---------- 53

3.5.1.2 ‘Yan Tasi ---------- 54

3.5.2 ‘ Yan A-cava masu Haya da Babura ---------- 55

3.6 Naxewa ---------- 57

Babi Na Huxu: Sigogin Hausar Kan Titi

4.1 Gabatarwa ---------- 58

4.2 Hausar Kan Titi---------- 59

4.3 Hausar ‘Yan Haya ---------- 61

4.3.1 Hausar ‘Yan Bas ---------- 61

4.3.2 Hausar ‘Yan A-cava ---------- 72

4.4 Hausar masu Sayar da Sayen Kayan sa Maye ---------- 85

4.4.1 Hausar ‘Yan Giya ---------- 87

4.4.2 Hausar ‘Yan Wiwi ---------- 93

4.4.3 Hausar ‘Yan Sholisho (Shava) ---------- 100

4.4.4 Hausar ‘Yan Qwaya ---------- 103

4.4.5 Hausar ‘Yan Kodin (Syrup) ---------- 106

4.5 Naxewa ---------- 110

Babi Na Biyar : Kammalawa

5.1 Taqaitawa ---------- 111

5.2 Abubuwan da Bincike ya Gano ---------- 112

5.3 Kammalawa ---------- 113

5.4 Shawarwari ---------- 115

Manazarta

Babi na Xaya:

Gabatarwa

1.1 Shimfixa

Al'ummar Hausawa al'umma ce daxaxxiya wadda ta kasance da harshenta wanda take gudanar da harkokinta na sadarwa tsakaninta da wasu al'ummomin da ba Hausawa ba. Harshen Hausa kamar kowane harshe a duniya na da kari wanda kowane rukuni na Hausawa suke amfani da shi. Wannan ya nuna cewa harshe muhimmin abu ne wajen tsara rayuwar kowace al'umma. Wannan ya sa wani masani ya bayyana ra'ayinsa kamar haka:

> *" Harshe wani muhimmin abu ne dake taka rawa ga rayuwar xan Adam, misali asali ma shi ne maqunshin tunanin xan Adam. Shi ya sa kowace al'umma, komin qanqantarta, komin lalacewarta, komin rashin wayewarta, tana da harshen da take amfani da shi a rayuwarta ta yau-da-kullum"* (Muhammad 2006:2).

Kamar yadda ya zo a faxar wasu masana:

> *"Harshen kowace al'umma yana bunqasa yana tumbatsa yana kuma havaka sanadiyyar cinikayya da auratayya da qaurace-qaurace, ya Allah ta fuskar yaqe-yaqe ko ta neman mafaka ko faxaxa qasa ko neman ilimi ko kuma fantsama a birane da zimmar neman aiki wanda hakan kan jawo qaruwar masu magana da harshen musamman ma idan ya kasance al'ummar da aka tarar masu magana da wani harshe ne na daban. Hakan na iya haifar da wani nau'in Karin harshe ko haxakar harshe ko kuma samar da wani nau'in harshe na daban"*
>
> *(* Zarruq da Al-Hassan 1986:12)

Akwai kare-karen harshe a Hausa iri biyu. Karin harshen yanki da karin harshen rukuni. Karin harshen yanki ya qunshi karin harshen da ake samu a tsakanin garuruwan Hausa, kamar Kananci da Zazzaganci da Katsinanci da Dauranci da Bausanci da dai sauransu. Karin harshen rukuni kuwa karin harshe ne da ya kevanta ga rukunan Hausawa masu gudanar da harkokin rayuwa daban-daban. Kamar yadda Muhammad (2006:2) yake cewa:

> *"Bayan masu sana'ar sadarwa ma, ai kusan kowace sana'a da ka sani a duniyar nan tana da irin tata*

> *gudunmuwar da take iya bayarwa ga harshe, don kuwa ita ce take samar da irin Hausarta ta musamman wadda takan yaxu ta zama mallakar kowane mai amfani da harshen, sana'arnan ta gargajiya ce kamar qira ko saqa ko dai ta zamani irin su kanikanci. Hasali ma dai, duk mai amfani da harshe yana da irin gudunmuwar da yake bayarwa wajen raya harshen, don kuwa ko kare ma da ranarsa"*

Wani muhimmin abu da ya kamata a yi la'akari da shi dangane da karin harshen Hausar rukuni shi ne tushensa da bazuwarsa da kuma bunqasarsa duk na nahiya ne, wato dai karin harshen rukuni da bazar na nahiya yake rawa. Kuma bayanan duk ya ta'allaqa ne a kan wannan vangare don kuwa duk abin da za a yi tsokaci sun shafi halin zamantakewar wasu mutane ne masu sarrafa harshe iri guda a tsakaninsu. Harshen Hausa na biya wa Hausawa buqatocinsu na sadarwa, kamar yadda Amfani (2011:2) ya bayyana:

> *"Harshen Hausa harshe ne daxaxxe, kammalalle kuma yalwatacce wanda yake biya wa Hausawa buqatarsu ta sadarwa da sauran vuqatoci na yau da kullum. Harshen Hausa harshe ne isasshe wanda kuma babu irin nazarin da masana ba su yi ba a kansa. Harshen Hausa harshe ne mai farin jini wanda a yau akwai mutane fiye da miliyan ashirin waxanda suka iya shi, kuma suna amfani da shi. Harshen Hausa fitaccen harshe ne domin kuwa ya watsu a duniya, kuma babu nahiyar da ba a san Hausa ba"*

Harshe shi ne magana ko furuci wanda ya bambanta mutum da dabba. Da harshe ake yin sadarwa da shi kuma ake qulla dangantaka ko abota tsakanin mutane, irin harshen da mutum yake amfani da shi a yanayin magana na nuna irin yanayin rayuwar mutum da asalinsa da jinsinsa da shekarunsa da ma sana'arsa. Harshe muhimmin abu ne domin da shi ake gudanar da

harkokin da suka shafi al'ada da tattalin arziki da siyasa da ilimi da kuma addini. Wannan ya haifar da samun rukuni na masu sana'a.

Rufa'i (1979) "harshe shi ne tunanin xan Adam wanda ake bayyanawa da baki ko da rubutu. Harshe wani tsari ne na furuci wanda xan Adam yake amfani da shi domin sadarwa tsakaninsa da wani xan Adam".

Galadanci (1980:331) " Harshe shi ne dillalin zuci mai bayyana abin da zuciya take so ko take qi. Irin abubuwan da harshe yakan bayyana a sarari don a fahimci mutum, shi ake kira magana ko zance".

Fagge, (2002) ya ce:

> *"harshe wata hanyar sadarwa ce da xan Adam yake amfani da sauti mai ma'ana wanda kuma yake bin wasu dokoki. Ya ce ta hakan ne kowacce al'umma da ke zaune a doron qasa take sadarwa kuma ta fahimci abubuwan da ke qunshe a zukatan jama'a kamar tunani da ra'ayi da hikima da sha'awa da dai sauransu"*

Yakasai, (2012:47) *ya ce:*

> *"harshe shi ne hanyar furta ma'anoni da tunane-tunanen da suke ran xan-Adam. wato dai ita ce hanyar sadarwa tsakanin mutane. Ita wannan hanya kuma ba ganinta ake yi ba, jin ta ake yi kawai, wato hanyar sadarwa ta xan-Adam (harshe) saututtuka ne masu ma'ana da ake furta su, kunnen mai sauraro ya ji, kana basirarsa ta kama, ta fahimta domin amfaninsa".*

Tun da mun ji harshe yanzun za mu ji abin da masana da manazarta suke cewa a kan Hausa da Hausawa.

Adamu, (1977) Hausa suna ne na harshe kuma masu wannan harshe ake kira Hausawa.

Amfani (2011:2) Hausa harshe ne, kuma Hausa tana xaya daga cikin harsunan xan Adam waxanda ake samu a nahiyar Afirka.

Skinner (1968:253-257) ya bayyana Hausa a matsayin harshe wanda al'ummar da ake kira Hausawa ke amfani da shi a matsayin hanyar sadarwa. Haka kuma ya yi waiwayen asalin kalmar ta Hausa da yadda ake kallon kalmar, misali Hausa na nufin qasar Gobir ko Have ko Gambari.

Hausar kan Titi kinaya ce da aka yi wa kalmar titi da ke nuni da wani nau'i na Hausa da ake samu a tsakanin rukunin Hausawa masu gudanar da harkokin rayuwarsu na yau da kullum a kan titi ko ba a kan titi ba. Irin wannan Hausar ta masu sana'o'i da masu aikata laifi ko shaye-shaye ana yin ta a ko'ina, abin nufi a kan titi ko a kasuwa ko a mashaya ko a makaranta ko a fada, kai har ma a masallaci a wasu lokuta, a kan sami irin wannan nau'i na Hausa. Abin lura da wannan nau'i na Hausa shi ne batu ne na muhalli da kuma manufar sadarwa, ba batu ne na rashin xa'a da rashin kunya da rashin sanin yakamata ba. Karin harshe ne da ake yi a lokacin sadarwa don cimma burin sadarwa ta hanyar aro da qirqira na kalmomi da ma jimloli da kan voye ko saye ko sakaya maganar ta xauki wata ma'ana wadda ba ita ce a sarari ko a zahiri ba, amma tana da wata ma'ana daban da ake nufi.

Hausar Kan Titi nau'i ce da wasu rukunin Hausawa kan yi amfani da karin harshen Hausa don sadarwa. Kamar yadda Babanzara (2006) ya bayyana karin harshen rukuni a matsayin zaurance. Xantumbishi (2003 da 2011) karin harshen rukuni a matsayin sara. Wurma (2002) ya yi

magana a kan faxaxa ma'ana ko taqaita ma'ana, inda ya bayyana shi a matsayin wani fanni mai nuna cigaban harshe.

Ke nan, Hausar Kan Titi kinaya ce da ke bayyana wani nau'i na Hausa da ake amfani da karin harshen rukuni da wasu Hausawa ke yi don sadarwa da niyyar saye ko voye wani ko wasu muhimman saqwanni da suka danganci harkokin rayuwarsu na yau da kullum, ta hanyar sana'a ko ta hanyar aikata laifi ko abin assha . Ana yin wannan karin harshe ne don a vad da bami, ko a cuci ko a yaudari mutum wanda wannan rukuni na mutane ko majiya harshe xaya suke yi ta yadda sai xan hannu kawai kan gane, ko ya fahimci ma'anar abin da aka faxa ko ake nufi. Wannan nau'i na Hausa kan tafi da zamani domin kuwa yawancin kalmomin na samuwa ne daga tsofaffin da aka sani da, da kuma waxanda ake amfani da su a yau duk da yake ma'anar da ake nufi daban da ma'anar da aka saba. Watau, ma'anar da ake nufi na tasowa ne daga waxannan kalmomi sai a samar ko a qirqiri sabuwar ma'ana. Saboda haka Hausar kan titi ba a na nufin nau'in Hausar mutanen banza ba ne, a'a abin nufi da haka shi ne Hausar da ba a saba yi yau da kullum ba, musamman a tsararren muhalli kamar makaranta; kuma ba kowa ne kan fahimci ma'anar da ake nufi ba.

An tsara wannan aiki babi-babi har biyar. Babi na xaya na da taken gabatarwa. Babi na biyu waiwayen ayyukan da suka gabata. Babi na uku ke xauke da Mutanen kan Titi da sana'o'insu. Babi na huxu na da taken sigogin Hausar kan Titi, sai babi na biyar na da kammalawa.

1.2 Dalilan Bincike

An yi nazarce-nazarce da dama a kan Hausar rukuni ko in ce karin harshen Hausa na rukuni, sai aka lura cewa ba a kai hankali wajen yanayin Hausar masu haya da abubuwan hawa da ma wasu sana'o'i ba; musamman kan nau'in Hausar da suke yi. Watau, abin nufi kinaya da qirqira da aro da ma faxaxa ma'ana da a kan yi amfani da su da ke nufin wata ma'ana da ban da ma'ana ta yau da kullum.

Xalibai manazarta ba su cika kallon matsalolin da suke faruwa a qasar nan ba, su ce za su zurfafa nazari a kai da nufin shawo kan matsalolin. Sanin kowa ne a yau ba sai gobe ba matsalar shaye-shaye na ci wa gwamnati da al'umma tuwo a qwarya, sai a ka lura masu tu'ammuli da waxannan kaya na yin wani nau'i na Hausa wadda ba kowa kan fahimci inda aka dosa ba. Bincike irin wannan wanda ya shafi al'umma, yana da matuqar amfani domin zai taimaka wajen ganin an sami canji a kan matsalar shaye-shaye ta hanyar saurin fahimtar masu wannan aiki a lokacin da suke sadarwa.

An lura cewa, voye ko saye ma'anar kalma har ma da jimla muhimmin lamari ne a lokacin sadarwa; musamman idan akwai manufar kawar da hankalin wanda ko waxanda ba a buqatar su san inda aka dosa ko yin cuta da yaudara ko vad da bami.

Bincike a kan Hausar kan titi zai taimaka sosai wajen ilimantar da jama'a, don su fahimci ma'anar kalma da ma jimla da a kan samu a ciki ko yanayin Hausar a lokacin sadarwa. Yana da kyau a taskace irin Hausar domin ta hanyar nazarinsu ne zai sa ba za a manta da su ba. Haka

kuma dai, binciken zai bai wa waxanda ba su san su ba damar fahimtar su, waxanda suka fahimce su, za su qara tunawa da su.

An zavi a yi bincike ne a kan Hausar kan titi saboda yadda take da tasiri wajen samar da sababbin kalmomi daga tsofaffin da aka sani a da, ta hanyar qirqira da aro da faxaxa ma'ana ta kalma ko jimla zuwa sababbi da ba a san da su ba can da. Hakan na taimakawa wajen bunqasar harshe.

1.3 Manufar Bincike.

Kamar yadda yake a rayuwa kusan kowane abu yana da manufar da ta sa ake yi. Manufar wannan bincike ita ce:

A bayyana irin burgewa da tsima jiki da zaburarwa da karsashi da zaven kalmomi da aro da qirqirar kalmomi da a kan yi kinaya da su a cikin Hausar kan titi, waxanda kan taimaka wajen isar da saqo; ta yadda saqon zai kai ga cimma manufar abin da ake buqata a isar, ta hanyar voye ko saye ma'anar kalma da ma jimla.

Daga cikin irin wannan bunqasa da harshen yake yi shi ne harshen ya tashi daga harshen qabila zuwa harshen al'umma. Haka ta sa wannan bincike ganin yana da kyau a qara sanin irin baiwar da take cikin harshen Hausa wadda ta haifar da Hausar kan titi, domin masu nazari nan gaba su sami karsashin faxaxa bincike a kan abin da ba a faxa ba dangane da yadda Hausar kan titi take a lokacin sadarwa .

1.4 Tambayoyin Bincike

Wannan bincike ya qudiri aniyar amsa waxannan tambayoyi da ma wasunsu:

I. Shin akwai alaqa ta qud-da-qud tsakanin harshe da zamantakewar mutum ko mutane, ta fuskar sana'a wadda kan haifar da Hausar da wannan rukuni suke yi don sadarwa?

II. Shin akwai wata hanya da wasu mutane suke bi su sadar tsakaninsu da abokanin zamansu ba tare da kowa ya fahimci abin da suke nufi ba?

III. Shin akwai wata hanya da masu aikata ayyukan da al'umma ke qyamata suke bi su yi sadarwa ba tare da kowa ya fahimci ma'anar da suke nufi ba, kuma har su kai ga cimma manufar isar da saqon. Idan akwai, yaya hanyar take?

IV. Mene ne ya haifar da voye ko saye ma'anar kalma da ma jimla da masu Hausar kan titi suke yi a lokacin sadarwa?

V. Yaya zubi da tsarin jimlolin da suke amfani da su?

1.5 **Matsalolin Bincike**

Na daga cikin matsalolin da wannan bincike ya ci karo da su rashin wani bincike da ya haxa rukunin mutanen da aka yi aiki a kan su, domin aikin ya haxa garuruwa uku ne: wato, Zariya da Kano da kuma Sakkwato. An yi bayani a kan ‘yan a-cava da ‘yan wiwi a waxannan gururuwa. Masu waxannan harkoki na voye ma’anar abin da suke nufi wannan ya sa binciken ya sami cikas wajen tattaro bayanai domin da zarar sun fahimci yadda aka dosa sai su xauki wata turba.

Binciken ya fuskanci matsalar rashin ba da haxin kai daga ‘yan bas da sauran mashayan da aka yi bincike a kan su hakan ne ya haifar da yin amfani da hanyoyin tattara bayanai da aka yi binciken da su maimakon hanyar tambayoyi ga masu harkokin. Qarancin lokaci da kuxi na cikin matsalolin da aka ci karo da su.

Rashin wayewar kai da gurguwar fahimtar masu waxannan harkoki da aka yi bincike a kan su ya haifar da matsala matuqa. Domin tunaninsu shi ne ana qoqarin a san sirrinsu ne wanda hakan zai sa a riqa saurin fahimtar Hausar da suke yi a lokacin sadarwa, ganin voye ko saye ma’anar kalma ta asali zuwa wata daban da ba ita ce ba, ita ce manufarsu ta qirqirar wannan karin harshe. Sanannen abu ne cewa waxannan masu harkokin rayuwa, kan yi amfani da karin harshen da ya kevanta da su wanda ba kowa kan san abin da suke nufi ba.

1.6 Muhimmancin Bincike

Ana fatan wannan bincike ya kasance mai matuqar muhimmanci, musamman ma ga xaliban nazarin harshe domin su daxa fahimtar tagomashin da harshen Hausa ke da shi.

Sanannen abu ne cewa babu wani cigaba da za a samu a kowane fanni na rayuwa sai da harshe. Harshe ne tubalin ginin fannoni na ilimi daban-daban. Ana amfani da harshe musamman ma harshen Hausa wajen harkokin addini da kasuwanci da sana'o'i da tattalin arziki a tsakanin al'umma da ma gudanar da mulki da siyasa da dukkan sauran vangarori na rayuwar Hausawa a ciki da wajen qasar Hausa.

Bugu da qari, ana fata manazarta halayyar zamantakewar xan-adam su ma su amfana da wannan bincike, a matsayin majingina wajen bayyana ko fasalta maganar Hausawa da harshen Hausa. Zai kuma amfani xalibai da manazarta tattalin arzikin qasa. Haka dai wannan bincike zai taimaka wajen qara samar da kayan nazari ga masu bincike musamman a fagen nazarin karin harshen Hausa na rukuni. Daxin daxawa, ana sa ran cewa wannan bincike ya amfani Hausawa da waxanda ba Hausawa ba; musamman masu sha'awar harshen Hausa da sharhi a kan harshen Hausa da Hausawa.

Wannan bincike zai taimaka wa hukumomin gwamnati kama daga Hukumar Yaqi da Hana Sha da Safarar Miyagun Qwayoyi da Jami'an 'yan sanda da Jami'an shige-da-fice da Jami'an kwastan da ma Jami'an tsaro na farin kaya wajen fahimtar yanayin sadarwar masu laifi a tsakanin Hausawa, musamman masu ta'ammali da kayan da kan sa maye.

1.7 Hasashen Bincike

Wannan bincike na sa ran tabbatar da cewa harshen Hausa sha-kundum ne ta yadda kowane rukuni na Hausawa da suke amfani da harshe, na yin haka ne don bayyana harkokin rayuwarsu; ta hanyar qirqirar kalmomi da ma jimloli da ake amfani da su wajen voye ko saye ma'anar da ake nufi ko kuma faxaxa ma'anar kalmomi. Haka kuma mai amfani da harshe kan kasance na gari ko lalatacce mai aikata laifi, hakan ke haifar da zavi ko qirqirar karin harshen da za a sadar da shi. Kamar yadda ake bin titi ko kan titi don zirga-zirga ko kai-kawo na mutane da makamantansu.

1.8 Hanyoyin Gudanar da Bincike

Wannan aiki an yi amfani da muhimman hanyoyin gudanar da bincike da aka amince da su, a tsarin gudanar da bincike irin wannan. Kashi na farko na waxanda ake aiki a kan su, su ne masu haya da abubuwan hawa da suka haxa da 'yan bas da 'yan a-cava, sai vangare na biyu masu saye da sayar da kayan sa maye. Hakan ya haifar da amfani da waxannan hanyoyi kamar haka:

Xakin Karatu: An yi amfani da xakunan karatu wajen gudanar da wannan bincike, daga ciki akwai xakunan karatu da ke Jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya da na Jami'ar Bayero da ke Kano da kuma Jami'ar Usmanu Xanfodiyo da ke Sakkwato. An duba kundayen bincike na neman digiri tun daga na xaya har zuwa na uku waxanda suke da alaqa ta kusa da ta nesa da wannan bincike, duk da yake kundayen bincike na digiri na xaya guda xaya ne kawai aka duba. Haka kuma an yi amfani da litattafai da aka wallafa da mujallu da ma qasidun da masana daban-daban suka rubuta musamman waxanda suke da nasaba da wannan aiki.

Ganawa: Binciken ya yi amfani da hanyar ganawa da tattaunawa da masana da masu hurxa da kuma masu harkoki da suka danganci abubuwan da ake bincike a kai.

Ziyara: An ziyarci wuraren da ake gudanar da harkoki na haya da abubuwan hawa da kuma saye da sayar da kayan sa maye domin samun gamsuwa da qarin bayani game da yanayin Hausar da suke yi. A cikin wuraren da aka ziyarta, akwai ofishin Hukumar Hana Sha da Fataucin Miyagun Qwayoyi da ke Zariya, sai tashoshin mota da kuma mahaxar 'yan a-cava a Zariya da Kano da kuma Sakkwato.

Sauraro: An saurari shirin dandalin matasa na gidan rediyon muryan jama'ar Jamus (DW Radio) da kuma wasu shirye-shirye na wasu gidajen rediyo. Dalilin yin haka kuwa shi ne wannan shiri ne da ke bayyana halin da matasa suke ciki ta fuskar zamantakewa, musamman shaye-shayen kayayyakin da ke sa maye.

1.9 Farfajiyar Bincike

Wannan bincike ya tsunduma ne wajen nazarin Hausar da ta danganci wasu rukunin Hausawa. Wato, Hausar masu haya da motoci 'yan bas da masu haya da babura ('yan a-cava). Akwai Hausar da ta shafi masu sayar da sayen kayan maye da suka haxa da mashaya giya da wiwi da shava da qwayayoyi da kuma kodin ko zumar kemis.

An iyakance wannan aiki ne a vangarori da wuraren da aka ambata a sama. Saboda haka, duk wasu bayanai da misalai an iyakance su ne a waxannan fannoni da aka ambata a baya. Binciken ya duba garuruwa uku ne ta fuskar masu haya da babura ('yan a-cava) da kuma 'yan wiwi. Sai 'yan bas da mashayan giya da shava da qwaya da kuma kodin ya taqaita a garin Zariya ne kawai.

1.10 Ma’anar Wasu Kevavvun Kalmomi

1.10.1 Sulo shiga cikin maye da mashaya maganin tari suke yi da manufar yin maye.

1.10.2 Kodin wani nau’i ne na maganin tari da ake sha ta hanyar wuce qa’idar shan maganin da manufar a yi maye.

1.10.3 Zumar kemis suna ne da mashayar maganin tari suka qirqira suke kiran maganin tari da shi.

1.10.4 Shava Shava na cikin rukunin kayan maye da ake shaqa. Shava na nufin aikata wani abu na wauta (Qamusun Hausa, 2006:405). Amma sholisho ko shava a nan na nufin wani nau’i na kayan shaye-shaye da ake sha da manufar yin maye. Sholisho ya samo asali ne daga sinadarin da ake yin faci ko liqin tif na keke ko na mashin da shi.

1.10.5 Qwaya/Qwayoyi Shan qwaya shi ne shan qwayoyi waxanda a likitance bai zama dole ba ko kuma a sha fiye da qima da kuma shan qwayoyi waxanda doka ta haramta a yi amfani da su, wiwi da hodar Iblis wato coceine da makamantansu (Gidan Dabino, 2012 :11).

Akwai qwayoyi ko magunguna waxanda suke haramtattun magunguna ne kuma doka ba ta aminta mutum ya mallaka ba, ko kuma ya yi amfani da su ba sai da umurnin likita (Popoola, 2011).

1.10.6 Maye: Maye na nufin tangaxi saboda shan giya ko wani abu mai bugarwa. (Qamusun Hausa, 2006:343).

1.10.7 Shaye-shaye N.D.L.E.A (2004:4) Shaye-shaye na nufin shan kowani irin sinadari wanda da zarar an sha ko an yi amfani da shi kan haifar da canji ko sauyi na xabi'a da tunani da gusar ko kawar da hankali, wanda kan haifar da maye ga wanda ya sha.

Shaye-shaye na nufin nanata shan abubuwa musamman masu sa maye (Qamusun Hausa, 2006:410).

1.11 Naxewa

A wannan babi mai taken gabatarwa an fara ne da kawo dalilan bincike da manufar bincike da tambayoyin bincike da matsalolin bincike da muhimmancin bincike da hasashen bincike sai kuma hanyoyin da aka bi wajen gudanar da wannan aiki, sannan farfajiyar bincike da kuma ma'anar wasu kevavvun kalmomi.

Babi na Biyu:

Waiwayen Ayyukan da suka Gabata

2.1 Gabatarwa

Hausawa dai kan ce “waiwaye adon tafiya, kuma da na gaba ake gwada zurfin ruwa”. Saboda haka, wannan aiki ya yi waiwaye da bitar ayyukan da malamai da manazarta da kuma masana suka yi masu alaqa ta kusa da ta nesa da wannan aiki ta fuskoki da dama komai qanqantarsu domin samun tudun dafawa.

2.2 Waiwayen Ayyukan da aka yi a kan Hausar Rukuni

Shi karin harshe na rukuni wani vangare ne na karin harshe da ya danganci wasu mutane masu halayyar zamantakewa da kuma hanyoyin sarrafa harshe iri guda, wato yanayin zamantakewarsu yana da nasaba da tasirin harshe da kuma yadda suke amfani da shi (Fagge, 1982).

2.2.1 Litattafai

Fagge, (2004:17 da 19 da 35 da 63) ya bayyana yadda ake samun sauye-sauye ta hanyar saye da qirqira a cikin harshe wanda ya haifar da ire-iren karin harshen Hausa na rukuni. Ya yi bayani a kan rukunoni da dama waxanda suka danganci masu sana’o’i mabambanta da sabgogin rayuwa na yau da kullum. Daga ciki akwai Hausar masu neman ilimi da malamai da ‘yan siyasa. Waxannan sun qunshi Hausar almajirai da Hausar gardawa da Hausar ‘yan qadiriyya da Hausar ‘yan tijjaniyya da Hausar ‘yan shi’a da Hausa ‘yan izala da Hausar xaliban Jami’ar Bayero da ke Kano maza da mata da Hausar ma’aikatan asibiti da Hausar ‘yan siyasa da kuma Hausar ‘yan wasan kwaikwayo. Akwai Hausa a wajen masu sana’o’in gargajiya da suka qunshi Hausar ‘yan kayan miya da Hausar majema da Hausar marina da Hausar magina da Hausar maqera da Hausar mahauta da Hausar masu kifi da Hausar masu sayar da dabbobi da Hausar ‘yan mata da Hausar matasa na daba-daba da Hausar ‘yan kasuwa da Hausar teloli da Hausar masu shayi da Hausar

masu yankar farce da Hausar dillalan filaye da gidaje da Hausar ‘yan tasi da Hausar ‘yan motoci (masu sayar da motoci) da Hausar ‘yan babura da Hausar ‘yan a-cava da Hausar ‘yan cuwa-cuwar man fetur da Hausar ‘yan canjin kuxi da Hausar ‘yan kayan wuta da Hausar makanikai daga qarshe sai ya yi magana a kan Hausar ‘yan sanda.

Tabbas ko tantama babu akwai dangantaka makusanciya tsakanin ayyukin Fagge (2004) da wannan ta fuskoki mabambanta, wannan bincike na magana ne a kan nazarin Hausar kan titi, yayin da wancan a Kano aka gudanar kuma an yi magana ne a kan ire-iren karin harshen Hausa na rukuni da ya kevanta da kowane rukuni. Wannan bincike kuwa ya haxa garuruwan Zariya da Kano da kuma Sakkwato ne. Sannan an tavo abubuwar da shi Fagge bai tavo ba.

An yi xori a kan kalmomin da ya binciko. Wato dai, kalmomin da ya kawo ba a maimaita su a wannan bincike ba. Inda aka maimaita an bayyana cewa Fagge ya kawo su a aikinsa.

Yakasai, (2012:109-118) ya ce:

> “*Harshen Hausa yana da faxi da yalwa ta yadda har ya kai ga samar da kare-karensa masu daman gaske. Haka kuma, wannan yalwar tasa ita ce ta kai ga haifar da nau’o’in Hausa daban-daban. A nan abin*

> *da ake nufi da nau'o'in Hausa shi ne, irin yadda ake samun rukunonin jama'a a harshen Hausa. Amma kuma sai a iske kowane rukuni yana da nasu nau'in kalmomin da yake amfani da su wajen tasa Hausar. Wannan shi ne ya sa ake jin irin kalmomin da ake furtawa a Hausar rukunin 'yan tasha sun bambanta ainun da kalmomin da ake amfani da su a Hausar rukunin Malaman zaure. Haka kuma Hausar 'yan kasuwa, kalmomin da za ka ji ana furtawa a rukunin Hausar fadar sarakuna. Domin kowane rukunin jama'a da nasa kalmomin fanni, da yake amfani da su a sadarwarsa ta yau da kullum. Waxannan kalmomin fanni su ne suke fayyace wa mai saurare ko mai karatu rukunin da mai magana yake ko wanda yake magana a kai* ".

Yakasai (2012) ya kawo rukunan wasu jama'a tare da irin Hausarsu, sannan ya bayar da misalan kalmomin fanni da suka danganci kowane fanni. Ya kawo misalai daga rukunoni kamar haka :

a. Hausar 'yan kasuwa. Ya kawo kalmomin guda goma da suka haxa da saye da sayarwa da tayi da albarka da an-sallama da la'ada da iqala da ciniki da arha da kuma tsada.
b. Hausar sarakuna. Ya kawo kalmomin fanni na fada irin su, ranka ya daxe da mu muka ce da fadawa da fada da rangadi da fare da barori da jakadiya da hawan daba.
c. Hausar mawaqa. Ya kawo kalmomin fanni da ake amfani da su a waqa, kalmomi iri su, gulbi da sadauki da mai kwana kyauta da mai qarfin arziqi da bahagon zagi da ruwan faqo da gagarau da katakoro da farin komo.
d. Hausar malamai. Ya kawo kalmomin fanni da malamai suke amfani da su, kalmomi irin su, alfasha da al'aura da faqiri da musantawa da mavarnaci da duhuli ko jima'i da makamantansu.

e. Hausar dattijai. Ya kawo kalmomin da dattijai suke amfani da su, kalmomi irin su, mai xakina da makwanci da biyan buqata da kwanan aure da bari in yi kurari da makamantansu.
f. Hausar samari da ‘yan mata. Ya kawo kalmomi irin su: ya ya dai da ji mana da kai amma kin haxu da yaya-wai da bula ce da rabin rayuwata da soyayya tsuntsuwa ce da malan yi hakuri da wai ka zalahoto da makamantansu.
g. Hausar matan aure. Ya kawo kalmomi irin su : a yi dai mu gani da ai mata suna suka tara da sauransu.
h. Hausar gidan magajiya. Ya kawo kalmomi irin su, ke wag ga mai abin daxi da ke shegiyar gari da baqar ashana da zuma uwar zaqi da sauransu.

A qarshe Yakasai, (2012:119) ya kawo Hausar wurin zaman makoki, ya kasa su kashi biyu. Wadda ake yi a qofar gida da kuma wadda ake yi a cikin gida. Yakasai bai tavo lamarin da yake damun al’umma ba a yau wato harkar shaye-shaye musamman wiwi da kwayoyi da kodin ko zumar kemis.

2.2.2 Kundayen Bincike

Ashiru (2000) ya yi bincike a kan Hausar ‘yan kasuwa a binciken da ya gudanar ya karkasa kalmomi kashi-kashi, tare da kawo misalai waxanda ‘yan kasuwa ne suke amfani da su dama waxanda su masu sayan kayan kan yi amfani da su domin sadarwa a tsakaninsu.

Misali:

Kalma	**Ma'anar yau da kullum**	**Sabuwar ma'ana**
Salula	Wayar tafi da gidanka	Wata irin shadda ce
Xanmani	Xanmani	Kwastoman da ya zo sayen kaya amma kuma ya qi saye.
Xangezawa	Xangezawa	Mutanen da suka zo don vata ciniki
Tafi da shi	Tafi da shi	Rashin daidaitawa a ciniki/za ka iya jarabawa

A qarshe ya bayyana cewa akwai karin harshen da 'yan kasuwar suke amfani da su a kan kayansu da kuma abokanan cinikinsu, wanda idan an yi amfani da su wanda yake wajen kasuwar ba zai fahimci abin da ake nufi ba. Haka kuma su ma abokan cinikayyarsu (masu sayan kaya) na amfani da irin wannan karin harshe kan 'yan kasuwar, wannan ya sa 'yan kasuwar ba za su fahimci abin da suke nufi ba.

Xantumbishi, (2003:37) a aikin da ya gudanar ya bayyana ayyuka na farko-farko da aka yi a fannin ilimin walwalar harshe, kamar Kirk-Greene, (1930) da Maqarfi, (1985) da Abdulkareem, (1995) da kuma Okpanachi, (2000).

Xantumbishi, (2003:146) ya nazarci sara ta la'akari da shekaru da jinsi da matsayin ilimi ko rashin ilimi wanda kan haifar da yin sara a lokacin sadarwa. Wato kalmomin da ake amfani da su a wurare na musamman da halin da ake ciki wanda kan haifar da yin sara, ba Hausar da aka saba

yau da kullum ba. Ya cigaba da cewa "Sara ko kalmomin da ake yin sara da su na bayyanar da yanayin rayuwa ta fuskar zamantakewa da hidimomin yau da kullum da kuma cigaban qere-qeren zamani da aka samu kai a cikin rayuwa". Ya kalli sara ta fuskoki kamar haka: Sara ta gaba xaya da sara da ta jivanci wani abu na musamman.

Dangane da sara da ta jivanci harkar ilimi da masu ilimin boko suke yi wanda yake bayyana hali ko yanayi da masu yin sarar suke sadarwa.

Misali :

Ma'ana a Hausa	**Ma'ana a sara**
Lashe (lick)	Ya ci jarabawa/ Ya ci zave
Haye (cross over)	Ya ci jarabawa
Kwaro (insect)	Mai Qoqari
Bindiga (gun)	Faxuwa jarabawa
An ga wata	An sami tambayoyin jarabawa kafin a yi
Buxe-wuta	Mayar da hankali kan karatu

(Xantumbishi, 2003)

Idan an lura za a ga cewa ma'ana ta zahiri ta sha bamban da ma'ana a wajen masu wannan Hausa ko sara, kamar yadda ya kira. Sara da ta jivanci ko danganci kuxi. Ya kawo misalai na kalmomi irin su, "bagi da qarfe da jinga da gada da boza da 'ya'yan banki da damawa da shafa-kai da akwai-shi da kacima" da makamantansu. Kalmomin sara da suka jivanci shaye-shaye. Ya kawo kalmomi irin su, "rushe da kwaxe da qole da gari da kuma daidai".

Xantumbishi (2003) ya cigaba da bayyana cewa, akwai tarayya wajen amfani da wasu kalmomi tsakanin masu ilimi mai zurfi da matsakaicin ilimi kai harma da marasa ilimi matuqar a wajen harkan shawo ce. Akwai kuma waxanda karuwai ne kawai suke amfani da su a cikin mata, amma a maza hakan kan yi qaranci; sannan samari ko matasa ‘yan shekaru 20-29 da 30-39 su ne kan gaba wajen yin wannan sara.

Dangane da sara da ta jivanci lalata ko fasiqanci ya kawo misalai na kalmomi irin su, “wake da qere da buge da amsa da hutu da shata da tava da goge da faqo da qishi da mota da faxo da gurza da miqe da gama da casa da yi-shi da Tana-ja” da makamantansu. Ya cigaba da cewa. “Ya wake”. Ba shi da ma’ana a Hausa sai dai abin da suke nufi shi ne. ”Ya sadu da ita”. Ya qara da cewa matasa su ne suka fi amfani da wannan sara kuma sun yi tarayya tsakanin masu ilimi da marasa ilimi wajen yin wannan al’amari, kuma mazan ne suka fi amfani da wannan sara.

Akwai sara da ta jivanci ko danganci sutura ya kawo misalai na kalmomi irin su, ”lashe da haxu da Ta-zarce da xige da cakare da gangariya da fes-fes da zuba da futo” da makamantansu. Sara da ta jivanci abinci ya kawo kalmomi irin su, ”wake da watu da gabza da garau-garau da wasko”. Sara da ta jivanci motocin hawa; ya kawo kalmomi da suke bayyana sunayen motoci irin su, “bana-ba-harka da dafa-duka da shiga-da-alwala da shiga-ba-biya da raja da makauniya” da sauransu. Sara da ta jivanci wasanni; ya kawo kalmomi irin su, “yanka da caji da kulle da tava da cizo da qeta da taka-leda da sake-lale da akwai-kai da yana-da-kyau“ da makatantansu.

Haka dai ya kalli sara wadda take ba ta rukuni ba, sara ce da ake yi domin biyan buqatar sadarwa da bai ta’allaqa ko bai jivanci wani rukuni ba ko wani abu na musamman ba. Amma wannan

nau'i na bayyana abubuwan rayuwa ne na yau da kullum waxanda ba su shafi rukunin da aka bayyana a kashi na farko ba. Ya kawo misalai na kalmomin da suka shafi harkokin rayuwar yau da kullum na kowane fanni na rayuwar xan'Adam. Misali, kalmomi irin su, "vagas da yab da murxe da share da manta da latsa da qoquwa da buta da jirga da wanki da kwaxar da yawa da gangara da daru da bagu da yarfa da vararwa da zare da zara da kifar da qazami da ta-tashi da banga" da makamantansu.

A taqaice binciken Xantumbishi, (2003) ya yi la'akari da waxannan abubuwa kamar haka :

I. Kalmar da aka ambata. Wato sarar da aka yi
II. Ma'anar kalma ta asali
III. Ma'ana a sara wadda take nuni da bambanci na magana a lokacin sadarwa.

Binciken da Xantumbishi ya gudanar (2003) na da alaqa da wannan qud-da-qud sai dai sun sha bamban a wurare kamar haka. Hausar masu motocin haya da Hausar mashaya da suka qunshi 'yan giya da 'yan wiwi da 'yan qwaya da sauransu. Ya kalli sara ta vangarori biyu, sara ta rukuni da sara wadda ba na wani rukuni ba. Yayin da wannan bincike ne a kan Hausar kan titi ta fuskoki biyu da suka qunshi Hausar 'yan haya da Hausar masu saye da sayar da kayan sa maye. Kabir (2004) a binciken da ta gudanar ta nuna cewa matsayin ilimi na boko da na addini ya kawo qirqire-qirqiren sababbin kalmoni da kuma canjin ma'anar kalmomi da jimloli tare da ingausa bisa matakai daban-daban. Haka kuma rashin ilimin boko ko na Isilamiya a wajen matasan mata bai hana su amfani da karin harshen nasu ba lokacin da suke so su yi hulxa da junansu.

Binciken Kabir (2004) ya gano cewa wannan karin harshen na faruwa a rukunin waxannan mata matasa, masu ilimin boko da na Isilamiya da kuma masu talla. Akwai sababbin kalmomi da aka qirqira a harshen Hausa, hakan ya samar da kalmomi da jimloli da aka qirqira ta hanyoyi daban-daban. Wasu ta hanyar faxaxa ma'ana, wasu ta hanyar ingausa.

Misali:

Kalma/jimla	**Ma'anar/Asali**	**Sabuwar ma'ana**
Muguwa	Mace mai mugunta	Yarinya kyakkyawa
Jar mota	Mota mai jar kala/fenti	Jinin haila (al'ada)
Akuya	Dabba	Yarinya mai samari da yawa
Abar garin	Sanannan abu da aka sani a cikin gari	Audugar mata da suke amfani da ita

(Kabir, 2004).

A qarshe an rarraba kalmomi da jimloli da aka binciko an kuma nuna tasirin harshe na biyu kan harshe na farko, wanda hakan ya samar da karin harshe na rukuni. Aikin Kabir (2004) na da alaqa da wannan aiki domin wannan na qoqarin bayyana Hausar kan titi, ta hanyar aro da qirqira da fassara da kan bayyana kinayar da aka yi da kuma ma'anar da ake nufi a lokacin sadarwa. Duk da ta fi mayar da hankali a kan qirqirar kalma, amma akwai faxaxa ma'ana ta hanyar kinaya.

Yakasai (2004) *ya* nazarci yadda sojoji suke samar da kalmomi ko jimloli a cikin bariki. Ya ce akwai kalmomin da suka shafi muqaman soja da abin ci da na sha da kuma waxanda suka shafi sauran hulxoxin rayuwa. Haka kuma, ya kalli yanayin kalmomi da jimloli da sauran mazauna barikokin suka samar wa harshen Hausa, kamar matan sojoji da ‘ya’yansu maza da mata da kuma yanayin Hausar sojojin da suka daxe suka tsufa cikin harshen Hausa.

Misali:

Kalma/Jimla	**Ma’ana ta Asali**	**Sabuwar Ma’ana**
Tsauni	Dutse mai tsawo ainun	Sabon shiga aikin soja
Ice ba ganye	Kwauren bishiya	Soja maras igiya
Magajiya	Uwar xakin karuwai	Muqami ne a wajen matan aure na Bariki
Bodar Kuwaiti Akwai takarda	Kan iyakar Kuwaiti A na cigiyar abin rubutu	Hanyar zuwa mami . salon saye wa idan ana son karvan bashi
Ya tava ruwan Kwara	Ya tava ruwan Kogin Kwara	Ya sha giya ke nan
Matar arsan ta yi ciki	Matar arsan tana da juna biyu	An sami cakin biyan albashin sojoji

(Yakasai, 2004)

A qarshen Yakasai (2004:245) ya gano cewa ra'ayin sojoji ya zo xaya dangane da yadda suke amfani da harshen Hausa, domin kuwa sun bayyana cewa "duk da cewa kasancewar rayuwar bariki hatsin bara ce, amma sun yi tarayya ta fagen amfani da harshen na Hausa; musamman saboda sauqinsa da shahararsa da kuma kasancewarsa zakaran gwajin dafi. Sun bayyana cewa yadda ake faxarsa haka nan ake rubuta shi savanin waxansu harsunan da suke nasu ne na asali".

Dawakin Tofa (2005) ya yi bincike a kan mahauta, ya ce "mahauta na da abubuwan bincike masu sha'awa, sana'arsu cike take da maganganu masu hikima da abubuwan alfahari, saboda fasahar da ke cikinta. Daga cikin waxannan tarin maganganu nasu akwai karin harshen mahauta. Shi wannan karin harshe na mahauta magana ce wadda ma'anarta ta bambanta da ma'ana ta asali wanda aka fi saninta. Wato, mahauta kan qirqiri wasu ma'anoni na daban da waxanda suke amfani da su saboda su sirrinta sana'arsu ta fawa. Ya cigaba da cewa shi wannan karin harshe ko kuma hanyar sadarwa ba wai wani karin harshen wata qasa ko wani gari ba ne na daban. A'a na rukunin wasu mutane ne da suka qaga wa kan su kawai sakamakon sana'a iri xaya da suke yi". Ya kawo karin harshen mahauta kamar haka: Na gama gari da na mahauta xaixaiku.

Na Gamagari

Kalma/Jimla	**Ma'ana ta Zahiri**	**Ma'ana a wajen mahauta**
Ni na yano shi	Ya fuce da hannu	Na riga ganin mai saye
Sai na ci kwala da bado	Cin kwala da bado	Neman la'ada wajen mai saye da mai sayarwa

Na Mahauta Xaixaiku

Ma da biyar	Ma da kuma biyar	Goma sha biyar
Na bayan qyaure	Wanda yake a bayan qofa	Xan qauye
Alhaji	Wanda ya je haji	Rago mai qaton ciki kuma fari

(Dawakin Tofa, 2005).

Muntari (2008) a binciken da ta gudanar a kan karin harshen rukuni a qasar Zazzau, ta fara ne da kawo tarihin qasar a taqaice da kuma bayanin karin harshen rukuni da dalilan da suke kawo karin harshen. Ta duba rukunoni da dama na masu sana'o'i mabambanta a qasar Zazzau, ta nazarci Hausar asibiti da Hausar 'yan a-cava da Hausar fada da Hausar kotu da Hausar mahauta. Ta kawo misalai na kalmomin da aka qirqira da kowane rukuni suke amfani da su waxanda suka kevanta da wannan rukuni kawai.

Bincike Muntari (2008) na da alaqa da wannan aiki. Sai dai a wannan aiki an kalli ire-iren 'yan a-cava da Hausar da suke yi da ke xauke kirarin da 'yan a-cava suke yi wa junansu da aro da kuma qirqira da ke cikin karin harshen rukuninsu a matsayin Hausar kan titi. Kuma an mai da hankali ne kan wasu sana'o'in da ake gudanarwa a kan titi da kuma matsalar da ta damu al'umma a yau ta shaye-shaye a Zariya da Kano da kuma Sakkwato. Baya ga haka an yi bayani a kan zubi da tsarin jimloli da ake samu a wannan nau'i na Hausa.

2.2.3 Muqalai

Abubakar (2001) ya yi bincike a kan Hausar gardawa a cikin birnin Kano da kewaye. Gardawa su ne almajirai da suka girma suka kai lokacin gardanta. Wato, bayan sun haddace Alqur'ani tare da iya rubuta shi. Ya kawo misalai na kalmomi da ma jumloli da suke amfani da su domin sadarwa. Akwai alaqa tsakanin aikin Abubakar da wannan aiki shi ne qirqirar kalmomi da ma jimloli da suke nufin ma'ana daban da aka saba, sai dai ya mayar da hankali ne a kan gardawa yayin da wannan ba gardawa ne aka yi bincike a kan su ba.

Fagge (2002:99-101) ya bayyana cewa akwai wani salon magana da zawarawa suke yi kuma ya kevanta da su ne kawai. Binciken ya nuna cewa su dai zawarawa a sanadiyar lokutan da suka xauka a gida kafin su samu damar yin wani aure shi ne yake haifar da ire-iren karin harshen da ake samu a tsakaninsu.

Ga wasu misalai kamar haka:

Kalma	**Ma'anar yau da kullum**	**Sabuwar ma'ana**
Xan birni	Wayayye	Matashin bazawari
Kwasa	Xibar wani abu	Aura
Qarfe	Qarfe	Marowacin bazawari

Tulu	Abin zuba ruwa	Bazawari mai qaton ciki

(Fagge, 2002:99).

Haqiqa akwai abubuwa da dama da karin harhsen ya haifar ga wannan rukunin na Hausawa. Kaxan daga cikinsu akwai, azanci wanda ya bai wa zawarawan damar sarrafa harshen Hausa ta vangarori daban-daban wanda yin hakan kan jawo laqawa wani abu suna, kuma ma'anar ta dace, kuma ta zauna daram ba tare da haifar da wata matsala ba a harshe.

Babanzara (2006:18-43) ya kalli karin harshen rukuni a matsayin zaurance wanda a kan koya a iya tsakanin matasa. Watau, wani rukuni na al'umma. Rukuni daban-daban na Hausawa na amfani da zaurance kuma suna yi ne da niyyar voye wani saqo ko wasu muhimman saqwanni. Kamar mashaya da masu laifi ko masu aikata laifi. Wani lokaci kuma ana amfani da zaurance domin yin zagi, tsegumi da gulma.

Ya ce:

> *"zaurance wani muhimmin batu ne ko al'amari ne a al'adar Hausawa'. Mai binciken ya kalli zaurance ta fuskoki kamar haka: zaurance na gaba xaya kamar a wajen hira ko talla da kuma zaurance na kinaya, ya bayyana irin wannan zaurance da cewa kowace jimla na da ma'anarta ta asali, a lokaci xaya kuma akwai ma'ana ta musamman; wanda sai xan hannu kan gane ma'anar da ake nufi. Wannan ne ma ya sa ake amfani da irin wannan zaurance domin a yaudari ko a cuci wanda bai san gaskiyar ko ainihin ma'anar da ake nufi ba".*

Misali:

Kalma/Jimla	**Ma'ana/abin da ake nufi**
Ba shi goron faranshi	Mare shi
Ya da qanwa	Nera xari da hamsin (#150)
Wasan yaran gano	Sata
Na je Saminaka	Na sami riba
Za ni Qaraye	Zan qara aure/ zan qara wani abu

(Babanzara, 2006:18-43)

Akwai kuma wasu misalai da ya kawo daga zaurancen zawarawa da zaurancen xalibai da zaurancen masu cuwa-cuwar man fetur da zaurancen mashaya wiwi da zaurancen dillalai da zaurancen fada.

Wannan bincike da Babanzara ya gudanar na da alaqa da wannan bincike domin suna magana ne kan wani nau'i na Hausa da ake yi a lokacin sadarwa da nufin kawar ko vad da hankalin wanda bai san abin da ake nufi ba. Ana yi ne da niyyar voye wani ko wasu muhimman saqwanni wanda mashaya da masu aikata laifi suke yi. Amma wannan an kira shi da suna Hausar kan titi ba zaurance ba. Sannan ba masu laifi ne kawai suke yi ba har da masu sana'o'i na yi a lokacin sadarwa, suna kuma yi ne da manufar kawar da hankalin masu sauraren su.

Musa (2011:273) ya fara ne da kawo ma'anar Hausa-Niga inda ya bayyana cewa "wani rukuni ne na matasa Hausawa masu haxin gambiza na al'adu biyu. Watau, al'adunsu na Hausa da na aro na Nigan Amerika wanda suke gani a fina-finan sinima da satilayi (dish) da bidiyo". Ya cigaba da cewa "bayan al'adunsu na asali, Hausa-Niga sun qirqiri sababbin kalmomi na sadarwa a tsakaninsu. Kuma waxannan kalmomi suna yin tasiri a tsakanin sauran matasa, kuma har suna samun karvuwa da bunqasa". Ya yi nuni da xabi'un Hausa-Niga da cewa aske kai qwalkwabo yana qyalli suna da shiga ta asali ta Hausawa. Akwai kuma shigarsu ta Amerika-Niga. Watau, T-shat marar hannu mai kama da singileti ko shat da wando jins koxaxxe ko mai jiki duk faci ko wanda yake qira cinos mai aljihu barkatai daga sama har qasa na yin zanzaro, da qaton takalmi sawu ciki (but), ko waje ko kambas. Wani lokaci Niga kan sa sarqa da xankunne. Hausa-Niga sun qirqiri kalmomin sadarwa waxanda suka kevanta da rukuninsu na matasa.

Misali:

Kalmar Niga	**Ma'anar Asali**	**Ma'ana a wurin Niga**
Tsami	Xanxano mai tsami	Rashin wayewar kai
Haxuwa/haxewa	Gamuwa	Yin ado
Sharewa	Kawar da datti	Mantawa/manta da shi
Mai tsada	Marar sauqi	Kyakkyawa/ji da kai

Django (Suna)	Dijango	Uba/mahaifi

(Musa, 2011:273-276).

Akwai alaqa tsakanin aikin da Musa (2011) ya gudanar da wannan domin suna magana ne a kan wani nau'i na Hausa da wasu rukuni na mutane ke yi don sadarwa da kan qirqiri kalmomi a harshe don sadarwa da manufar kawar da tunanin wanda ko waxanda ba su cikin rukuninsu. sai dai wannan aiki ya kalli saye ko voye ma'anar kalma da ma jimla da kuma aro wanda Musa bai bayyana su a fili ba.

Azare (2011:224) ya bayyana cewa mata na amfani da wasu nau'in kalmomin harshe domin sadarwa a tsakaninsu ta yadda ba kowane mutum kan fahimci ma'anar da suke nufi ba. Ya kalli rukunonin mata da dama, daga matan aure masu ilimi da mara sa ilimi, sai mata mara sa aure. Watau, 'yan mata masu ilimi na sakandare da 'yan jami'a da 'yan islamiya da kuma marasa ilimi kamar 'yan talla, sannan zawarawa da kuma karuwai. Kasancewar kowane rukuni na da irin Hausar da suke amfani da shi domin sadarwa a tsakaninsu. Ya kawo misalai kamar haka: na matar aure marasa ilimi da masu ilimi, mata marasa aure ('yan mata) masu ilimi na sakandare da jami'a da 'yan islamiyya, da marasa ilimi ('yan talla). Akwai kuma Hausar da ta danganci ko ta shafi zawarawa da karuwai da suke amfani da su a lokacin sadarwa.

Misali:

Kalma	**Ma'ana ta asali**	**Sabuwar ma'ana**
Sai da manja	Sayar da manja	Jinin haila
Rijiya gaba dubu	Rijiya gaba dubu	Macce mai yawan aure

Himma ce	Mace mai himmi	Maccen da ana mata aure da wata tara ta haihu
Daqiqi	Mutum mara fahimta	Ragon namiji
Waccar Magana	Waccar magana da aka yi	Saduwa da miji
Sandar girma	Sandar girma ta Sarki	Al'aurar namiji
Ba sabis	Babu sabis na waya	Mijin da baya biya wa matarsa buqata
Burodi	Abin ci burudi	Audugar al'ada

(Azare, 2011:221-232)

A qarshe, ya nuna cewa ko tantama babu domin kuwa a kan sami sauyi a harshe ta la'akari da yanayin hulxoxin al'umma, wanda kan haifar da qirqirar harshe, wato karin harshe domin ya dace da hali ko yanayin da ake ciki. Wannan kan haifar da samuwar sababbin kalmomi waxanda daga baya sukan koma ga al'umma. Watau, al'umma su zavi waxanda za su riqa amfani da su, su kuma yi watsi da wasunsu.

Wannan aiki da Azare (2011) ya gudanar na da alaqa da wannan aikin, domin suna magana ne a kan wata kevabbiyar ma'ana da zance ke da ita baya ga ma'anar da aka sani ta yau da kullum, kuma ma'anar kan buqaci bayani kafin a san abin da ake nufi. Akwai wani abin lura a nan domin Azare ya taqaita aikin a kan mata, yayin da wannan aiki an mai da hankali ne a kan Hausar kan titi da ya qunshi masu haya da abin hawa da kuma masu saye da sayar da kayan maye.

Xantumbishi (2011:149) ya kalli karin harshe na rukuni a matsayin sara, domin kuwa ai wani rukuni ne na wasu Hausawa da suke sadarwa a tsakaninsu da harshen Hausa kan qirqiri karin harshe ko sara domin hulxar sadarwa. Ya cigaba da cewa bincike na baya bayannan da Adamu (2002) da Bature (2002) da Xantumbishi (2003) suka gudanar ya nuna cewa matasa su ne kan gaba wajen bunqasa da bayar da gudunmuwa wajen ciyar da harshen Hausa gaba. Masu ilimi a cikinsu musamman samari kan qirqiri kalmomi waxanda suke amfani da su a lokacin sadarwa a tsakaninsu domin biyan buqatarsu. Ya kawo misalai na kalmomi irin su "*zarce* da *daidai-ta-saho* da kuma kalmar *haska*". Duka waxannan kalmomi sun sami sabuwar ma'ana na *ta-zarce* da *adaidai-ta- sahu* da kuma *haskashi*.

A qarshe ya nuna cewa sara na da matsayin karin harshe na Hausa kuma na rukuni. Dalili kuwa, rukunoni mabambanta na hulxar sadarwa a kowane lokaci, kuma amfani da sara ya kasance abin yi a kowane lokaci domin cimma buri ko manufar sadarwa. Sara ta kasance wani yanayi da yake nuni da rukunin da mai magana ko sara yake ciki. Haka kuma sara kan taka muhimimiyar rawa a harkokin zamantakewa da siyasa na Hausawa.

Ayyukan da Xantumbishi ya gudanar na da alaqa da wannan ta fuskar ma'ana da ake nufi na kalma baya ga ma'anar yau da kullum da aka san kalma da ita, kuma ya fi karkata ne a kan qirqiyar kalma da ma jimla da masu sara suke yi a lokacin sadarwa a birnin Kano; yayin da wannan bincike ya fi karkata a kan qirqira da aro da kinaya da ma'anar kalma da ma jimla ke nufi a lokacin sadarwa ba a Kano kawai ba. Sannnan kuma wannan bincike ne a kan Hausar kan titi ta fuskoki biyu da suka qunshi Hausar 'yan haya da Hausar masu saye da sayan kayan sa maye. An kuma yi bayani a kan zubi da tsarin jimlolin da azuzuwan aikatau da ke cikin jimlolin.

Ayyukan da suka gabata da wannan nazari ya duba, sun qara wa wannan aiki haske kasancewar akwai alaqar da ke tsakani ta kusa da ta nesa. Don haka dukan ayyukan sun bayar da babbar gudunmuwa ga wannan bincike.

2.3 Naxewa

Aikace-aikacen da aka yi bitar su, su ne waxanda wannan bincike ya ci karo da su waxanda suke da alaqa da wannan aiki ta kusa ko ta nesa. Kamar yadda bayanai suka gabata akwai kare-karen harshe da dama kuma waxansu suna kama da juna, wannan alaqa da ke tsakanin waxannan kare-karen harshen ya sa waxansu mutane kan xauka cewa karin harshen waxancan mutanen yana dai-dai da na waxancan. Amma abin da ya kamata a fahimta, a nan akwai wasu ‘yan bambance-

bambance tsakanin su musamman ta ma'ana. Nazarinsu ya taimaka wajen tsara alqiblar wannan aiki mai taken "Nazarin Hausar Kan Titi".

Babi na Uku

Mutanen kan Titi da Sana'o'insu

3.1 Gabatarwa

A san mutum a san cinikinsa', wannan babi zai yi magana ne a kan mutanen kan titi da sana'o'insu tare da rayuwarsu. Kasancewar kowace sana'a ita ce take samar da irin Hausarta ta

musamman wadda takan yaxu ta zama mallakar kowane mai amfani da harshe. Akwai kuma bayani a kan karin harshe da majiya harshe xaya da kuma dangantakar harshe da al'umma.

3.2 Karin Harshe

Idan aka ce karin harshe ana nufin bambance-bambance ne na sarrafa harshe xaya. Watau, bambancin da ake samu a cikin harshe xaya. Akwai kare-karen harshe iri biyu a harshen Hausa da suka haxa da karin harshen yanki ko lardi da karin harshen rukuni. Da yake wannan binciken yana qoqarin tattaunawa ne a kan karin harshe na rukuni, to, a nan an kawo ma'anar karin harshe na rukuni, a matsayin matashiya, Fagge (2002) ya xauko daga Bergery (1934) da Salim (1981) da Musa (1996) inda suka nuna cewa karin harshen Hausa yana da kare-kare na nahiya da kuma na rukuni amma a nan za a yi duba ne a kan karin harshe na rukuni. Karin harshe na rukuni wani vangare ne na karin harshe da ya danganci wasu mutane masu halayyar zamantakewa da kuma hanyoyin sarrafa harshe iri xaya, wato yanayin zamantakewarsu yana da nasaba da tasirin harshe da kuma yadda suke amfani da shi (Fagge 2002:97).

Hudson (1980:24) says:

> *"a language variety is a set of linguistic items with similar distribution. The foregoing definition has two advantages*
> *a) It allows the linguist to say that Nigerian English, English of the legal profession, and Standard English are all varieties of English language.*
> *b) It helps the linguist to treat all languages of a community as a single variety since all the linguistic items have a similar social distribution".*

"karin harshe nau'i ne na harshe da yake haifar da sakamako xaya na cimma burin sadarwa. Karin harshe na samuwa ba tare da wani cikas ba a cikin al'umma xaya ta fuskoki mabambanta, kama daga dalilin yin amfani da harshen, matsayin mai magana ko sauraran maganar da kuma saqon da ake son gabatarwa.

a) Domin a kan ce Hausar ko karin harshen lauyoyi da makamancin haka.

b) Hakan na ba masana ilimin harsuna su kalli harshe a matsayin abu xaya."

Sarari (1989:3) kuwa ga yadda yake ganin lamarin har ma yana cewa:

"Karin harshe wani nau'i ne na yadda wasu mutane suke amfani da harshen domin isar da saqo, ta hanyar yin amfani da wasu kalmomi ko ginin jumla ko qirar kalma, wanda wasu vangarorin ba sa amfani da su duk da cewa harshe xaya suke magana da shi".

Wales (1989:398) says:

"to obtain a given variety of language, three main variables are to distinguished which are felt to be very significant: Field (subject-matter), medium (speech or writing), and tenor (social role-which will influence the degree of mood)".

Wales (1989:398) *cewa ya yi:*

"za a iya samun kare-karen harshe ta la'akari da ko a dalilan abubuwa uku':

1) Gurbi ko batun da ake magana ko sadarwa a kansa.

2) Hanyar isar da saqon.

3) Yanayin da ake ciki wanda yake yin tasiri a kan kalmomin da za a zava domin sadarwa".

Ya cigaba da cewa dalili ko yanayi ne kan tilasta kaucewa daga daidaitaccen harshe zuwa yin amfani da wanda ba shi ba. Ke nan, wannan na nuni da cewa rukunin mutane da kuma batun da ake magana a kai su ne suke taka muhimmiyar rawa wajen samar da wani harshe. Watau karin harshe.

Akwai hanyoyi uku na fahimtar karin harshe:

1) Ta fuskar yanayin mai magana (furuci).
2) Ta fuskar kalma da ma'ana.
3) Ta fuskar ginin jimla.

Harshe abu ne na hulxa ta yau da kullum kamar yadda karin harshe yake. Wannan lamari na da alaqa da wannan aikin ganin cewa ana magana ne a kan kalma da ma'ana, wadda wasu masu magana kan yi amfani da ita don bayyana kansu da ma badda bami a lokacin sadarwa.

Zarruk da Al-Hassan da Adamu (1990) kuwa sun bayyana ma'anar karin harshe da cewa
"Yan bambance-bambancen lafazi da kalmomi da jumloli tsakanin rukunin al'umma ko shiyyoyin qasa ne, mai harshe xaya".

Karin harshe kalmomi ne na harshe waxanda ake amfani da su na musamman a wuraren sana'a ko aiki ko yanayi da aka tsinci kai. Harshen da ma'aikacin kiwon lafiya zai yi amfani da shi ya bambanta da harshen lauyoyi ko masu qere-qere za su yi amfani da shi, fitacciyar siffar ita ce ta bambancin ma'ana ta yin amfani da kalma mai nufin wata ma'ana ta musamman. Kamar yadda

Flexner yake gani duba Xantumbishi (2003:32-34). “Harshe na sajewa ko sauyawa a kowane lokaci da zaran an sami wani sabon tunani ko cigaba, hakan kan haifar da sababbin kalmomi”.

Fagge (2004:37) ya ce:

> *“ Karin harshen rukuni vangare ne na karin harshe da ya danganci halayyar zamantakewa da kuma hanyoyin sarrafa harshe iri guda. Wato, yanayin zamantakewa na tasiri na musamman dangane da harshe da kuma yadda ake amfani da shi”.*

Adam (2008) karin harshen rukuni wasu zavavvun kalmomi ne ko yankin zance na musamman wanda ake amfani da su a harshe domin bayyana wata ma’ana da ta kevanta da wannan rukuni.

Daga ma’anonin da bayanan da suka gabata da kuma yadda Babanzara (2006) ya bayyana ke nan karin harshe na rukuni wani sarqaqqen zance ne ko magana wadda wasu kevavvun mutane kan yi amfani da su ko masu wata sana’a ko qungiya mai wahalar fahimta. Daga cikin mutanen akwai varayi da xalibai da ‘yan boko da zaurawa da sauransu. Kar a xauka harshen Hausa ne kawai yake da kare-karen harshe a’a, ai duk wani harshe na duniya ana iya samun sa da karin harshe.

3.2.1 Majiya Harshe Xaya

Majiya harshe xaya batu ne da masana ilimin walwalar harshe suke amfani da shi domin nuni da al'umma masu harshe ko mutane masu yi da kuma jin magana da harshe iri xaya. Wannan ya haifar da ra'ayoyi da dama dangane da ma'anar majiya harshe xaya.

Gumperz (1962:386) says:

> "*defines a speech community as any human aggregate characterised by regular and frequent interaction by means of a shared body of verval sags and set off from similar aggregates by significant differences in language use".*

ya ce….

> *"majiya harshe xaya rukunin wasu mutane masu harshe xaya da suke zaune tare kuma suke yawan hulxa ta sadarwa da juna, sannan ake samun wasu 'yan bambance-bambance ta fuskar amfani da harshe a yayin da ake hulxa tsakaninsu da waxanda ba a cikinsu suke ba".*

Lyons (1970:326) "a speech community involves all people who use a given dialect. The criterion here is the absence of a cultural and social entity".

ya ce:

> "*majiya harshe xaya ya qunshi dukkan mutanen da suke amfani da karin harshe xaya. Ke nan' majiya harshe xaya rukuni ne na mutane da suke amfani da karin harshe iri xaya ba tare da la'akari da al'ada ba domin sadarwa a cikin al'umma xaya".*

Daura (1974) ya kalli majiya harshe xaya a Hausawa inda ya bayyana yanayin da Kanawa suke magana na nuna yanayin yadda suke hulxar kasuwanci.

Daba (1987) ya yi tsokaci a kan majiya harshe xaya a karin harshen kananci. Ya bayyana cewa akwai masu yin amfani da harshen Hausa a matsayin L1, L2 da kuma L3. Watau, masu harshen uwa da masu harshe na biyu da kuma harshen Hausa a matsayin harshe na uku.

Duka waxannan bayanai na qoqarin bayyana yadda wani yanki a cikin al'umma xaya, masu harshe xaya suke magana a tsakaninsu a lokacin sadarwa wadda a kan sami wasu 'yan bambance-bambance. Waxannan yanki na mutane a fahimtar Daba kan kasance masu harshen uwa ko harshe na biyu ko kuma harshe na uku.

3.3 Dangantakar Harshe da Al'umma

Allah (SWT) da ya yi mutane jinsi-jinsi sai kuma ya ba su hanyar da za su yi mu'amala da junansu, wato ta hanyar magana da harshe. Harshe na taka muhimmiyar rawa wajen isar da tunani da al'adun kowace al'umma. Akwai ma'anoni mabambanta da aka bayar a kan ma'anar harshe.

Abdullahi (1934:235) ya ce za mu iya ganin haka a wasu surori na Alqur'ani mai girma. Misali, Suratul Rum ta 30 Aya ta 22. Allah (SWT) Yana cewa:

> *"Kuma akwai daga ayoyinSa, halittar sammai da qassai, da savawar harsunanku, da launikanku. Lallai a cikin wannan akwai ayoyi ga masu ilimi"*

Sai kuma Suratul Hujurat ta 49, aya ta 13, Allah Yana cewa :

> *"Ya ku mutane ! lallai ne Mu, Mun halitta ku daga namiji da mace, kuma Muka sanya ku dangogi da qabiloli, domin ku san juna. Lallai mafificin daraja a wurin Allah (Shi ne) wanda Ya ke mafifici a taqwa. Lallai ne, Allah Masani ne, Mai qididdigewa".*

Osisanwo (2003:1) "language is a human vocal noise or the arbitrary graphic representation of this noise, used systematically and conventionally by members of a speech community for the purpose of communication".

Osisanwo (2003:1) "harshe wasu 'yan guntayen maganganu ne da xan Adam kan yi waxanda ake amfani da su tsakanin majiya harshe xaya domin tabbatar da an cimma burin sadarwa".

Xantumbushi (2004) "Harshe shi ne magana ko furuci wanda ya bambanta mutun da dabba. Ana fassara tunani da harshe, da harshe ake sadarwa da harshe ake qulla abota da kuma tafiyar da dukkan al'amurran rayuwa".

Yakasai, (2012:47) ya bayyana harshe da cewa:

> *"hanyar furta ma'anoni da tunane-tunanen da suke ran xan-Adam. wato dai hanyar sadarwa tsakanin mutane. Ita wannan hanya kuma ba ganin ta ake yi ba, jin ta ake yi kawai, wato hanyar sadarwa ta xan-Adam (harshe) saututtuka ne masu ma'ana da ake furta su, kunnen mai sauraro ya ji, kana basirarsa ta kama, ta fahimta domin amfaninsa".*

Tunda mun ji yadda masana ke kallon harshe yanzu za a karkata akalar bayani zuwa al'umma. Al'umma kuwa ita ce tarin xaixaikun mutane da suke zaune tare a gari guda, ko yanki ko lardi ko jiha ko qasa . Al'umma tana iya qunsar qabilu daban-daban. Wannan ya nuna cewa duk inda aka sami fiye da xan-adam guda a wuri guda, to lalurar hulxa da mu'amula ta kama. Hulxa da mu'amala kuwa ba sa cika ba tare da magana ba. Ke nan, amfani da harshe tilas ne a yi hulxa, kuma lalura ce. Tun da yake haka ne kuwa, to buqatar harshe ga xan-adam ta kai qarfin

buqatarsa ga abinci da ruwa, ko ma wataqila har da iskar shaqa (Rufa'i, 1986). Yayin da wani masani ya bayyana al'umma da cewa "Xaukacin mutanen da ke zaune a wuri xaya kuma suke da al'adu da xabi'u iri xaya" (Hornby, 1948).

Kalmar dangantaka na iya xaukar ma'anoni kamar alaqa, zamantakewa, qawance tsakanin abubuwa biyu ko fiye. Saboda haka, ta vangaren dangantaka muhimmancin harshe ga rayuwar xan-Adam ba abu ne voyayye ba.

Trudgil (1974:32-33) *stated that ……..*

> *"sociolinguistics is a part of linguistics concerned with language as a social and cultural phenomenon". Sociolinguistics is concerned with investigating the relationship between language and society with the aim of attaining a better understanding of the structure of a language and of how such a linguistic code functions in communication".*

Ya ce:

> *"Sadarwa ko isar da saqo ta bayar da bayani da kuma tabbatar da alaqa da dangantaka tsakanin jama'a. Ita dangantaka tana wanzuwa ne tsakanin xaixaiku da kuma al'ummomi. Masanin ya cigaba da cewa "bambancin tafiyar da rayuwa na bambanta al'umma fiye da bambancin shiyya".*

Al'umma kamar tilon xan-adam tana da alfahari da kuma buri. Alfaharin nan shi ne tarihi, buri kuwa shi ne kokawar rayuwa domin yau da kullum . Saboda haka, a fafutuka ta wanzuwa, akwai buqatar abubuwan nan da suka zama dole ga kowace al'umma domin rayuwa. Waxannan abubuwa su ne: mulki da shari'a da tattalin arziqi da ilimi da addini da kuma al'ada (Yakasai, 2012:51-54).

Akwai dangantaka mabambanta da take tsakanin harshe da al'umma kamar yadda masana suke gani.

Wardhaugh (1988:10) argues that, these conflicting ideas have produced four distinct theories:

I. *Social structure may influence or determine linguistic structure and bahaviour.*

II. *Linguistic structure and/ or behavior may determine social structure. This is the view behind the Sapir-Whorfian hypothesis, the theories of Bernstein, and related linguists, who argue that a language by itself could have an overriding power on the user, sometimes to the point of complete domination.*

III. *The influence is bi-directional: a form of symbolic relationship between language and the society.*

IV. *There is no relationship between language and a social organization, and that either form is directly opposed to the other".*

Wardhaugh (1988:10) na ganin cewa akwai abubuwa huxu da wannan batu na dangantakar harshe da al'umma ya gadar:

I. *Tsarin zamantakewa kan iya yin tasiri ko tafiyar da yadda harshe ko xabi'u kan kasance, akwai alamu da kan iya tabbatar da wannan tunani. Bambancin shekaru tsakanin wannan rukuni da wancan rukuni. Ke nan, wannan rukuni na mutane kan yi magana daban da na wancan rukunin mutane. Waxannan bambance-bambance kan kasance na yanki kai har ma da bambanci tsakanin maza da mata.*

II. *Harshe kan tafiyar da zamantakewar al'umma, wannan shi ya yi daidai da tunanin Sapir Whorfian, Beinstein da wasu. Sun ce "harshe shi kansa na iya tafiyar da yadda mai amfani da harshen kan yi amfani da shi". Yakasai, (2012) A wannan hasashe, cewa ya yi "harshe ya tanadar wa majiya wata dama ta hango duniya (harshe-linzamin-tunani) akasin yadda ake hangen sauran al'amura". Saboda haka, harshe yana tasiri kan al'umma ta hanyar daidaita tunanin majiya kan lamuran duniya.*

III. *Tasirin vangarori biyun wato harshe da kuma al'ummar kanta.*

IV. *Babu wata alaqa ko tasiri ta a zo a gani tsakanin harshe da zamantakewa domin kowanne na zaman kan sa ne.*

Wardhaugh (1988:10) ya ba da ma'anar ta qoqarin nuna dangantakar da take tsakanin zamantakewa da kuma harshe domin bayyana bambancin da kan faru a vangarorin biyu. Wannan na da alaqa da Trudgills (1974:32-33) Ilimin walwalar harshe vangare ne na nazarin harshe da yake kallon harshe ta fuskar zamantakewa da al'adar al'ummar da suke amfani da wannan harshe. Ilimin walwalar harshe na nazarin dangantakar da take tsakanin harshe da al'ummar da suke amfani da wannan harshe da burin tabbatar da fahimtar tsarin harshe da kuma yadda qa'idojin harshe suke a lokacin sadarwa.

Hudson, (1980: 4-5) has described the difference as follows:

> *"Sociolinguistics is the study of language in relation to the society, while the sociology of language is the study of society in relation to language".*

Hudson, (1980: 4-5) ya bayyana cewa:

> *"ilimin walwalar harshe na nazarin harshe ne da dangantakarsa da al'umma, ya yin da nazarin zamantakewar xan-adam da harshe yake nazarin al'umma da dangantakarsu da harshe".*

Ke nan, idan muna nazarin ilimin walwalar harshe muna qoqarin fito da yadda al'umma take magana da harshe ne domin gudanar da harkokin rayuwa ta yau da kullum. Hakan kan haifar da bambance-bambance a lokacin sadarwa.

Wannan ya yi daidai da tunanin Fromkin da Rodman (1978:272) suka ce "culture plays great role in dealing with language issues. This is because it determines the rules of social behavior".

Fromkin and Rodman, (1978:272) "al'ada na taka muhimmiyar rawa wajen tafiyar da harshe, saboda al'adarce take nuni da yadda zamantakewa take gudana.

Holmes, (2001) ya bayyana ilimin walwalar harshe a matsayin wani fage na nazari da kan nazarci hanyoyin da ake sarrafa harshe domin tantance qima da walwalar harshe gida biyu:

I. Masu nasaba da harshe.

II. Masu nasaba da zamantakewa.

Akwai batun shekaru da jinsi da muqami da kuma matsayin mai magana a cikin muhallin sadarwa. Muhalli yana xaya daga cikin ma'aunan walwalar harshe da yake da tasiri wajen zavin harshe ko karin harshen da za a yi sadarwa da shi. Matsayi ko muqamin mai amfani da harshe kan hana ambaton wasu batutuwa, ko kuma sun tanadar wa mai magana wani zavi na abin da yake so ya faxa. Dukkan waxannan ma'aunai masu nasaba da zamantakewa ne suna kuma da tasiri kan ma'aunai masu nasaba da harshe. Su kuwa ma'aunan walwalar harshe masu nasaba da harshe suna jagora ne wajen zavin harshe ko kuma karin harshe. Ma'aunai masu nasaba da zamantakewa kamar muhalli, sana'a da kuma shekaru ma suna da tasiri wajen zavin harshe. Shi kuma bambancin karin harshe yana shafar tsarin sauti da qirar kalmomi da jumloli ne. (Crystal da Davy,1969 a cikin Yakasai, 2012:66).

3.4 Ma'anar Kan Titi

Kalmar titi ta samo asali ne daga ingilishi wato *'street*'. Wanda Bergery (1934:1016) ya ce daidai yake da hanya. Hanya kuwa na nufin wurin da ake bi da qafa ko da abin hawa. (Qamusun Hausa, 2006:195).

Titi na matsayin wurin da mutane suke bi da qafa ko da abin hawa don gudanar da harkokin rayuwarsu na yau da kullun. Wajen da ake kai kawo na mutane da abin hawa na karfe ko wanda ba na qarfe ba. Kan Titi kuwa ya zamanto ko yana nuni da wurin da ake bi ne da qafa ko a abin hawa a lokacin zirga-zirgar mutane ko dabbobi a birni ko kuma a qauye daga wannan wuri zuwa wancan wuri, a gari xaya ko kuma a mabambantan gari.

3.4.1 Rayuwar Kan Titi

Rayuwa na da ma'anar cigaba da wanzuwa ko havaka ko kuma girma (Bergery,1934: 907). 'Allah xaya gari bamban'. 'Kai 'yan yara gumi na nake ci'. 'Kowa ya ci da mai kuxi nai'**.** An fara da wannan batu ne don qoqarin bayyana yadda rayuwan kan titi take. Rayuwar kan titi na nuni da yadda mutane suke qoqarin cigaba da wanzuwa a duniya ta hanyar kai kawo don neman abubuwan biyan buqatun rayuwa waxanda xan-adam ke buqata. Watau, kuxi da a kan yi amfani da su wajen saye da sayarwa na abinci da abin sha da sutura da magani da makamantarsu.

'In ba ka yi ba ni wuri'. Rayuwar kan titi, rayuwa ce ta ka zo na zo kowa ka gani na qoqarin nema ne ko ta hanyar da ta dace ko kuma akasin hakan, watau ta hanyar da al'umma ba ta aminta da ita ba. Rayuwa ce ta ba zama, a tsattsaye rayuwar take kowa kansa ya sani sannan wani ya biyo baya. Rayuwa ce da babu kunya sosai ga masu rayuwar da kan yi duk abin da suka ga dama matuqar za ta kai ga cimma manufarsu ta fitowa kan titi. Wannan ya haifar da mutane iri-iri ta fuskar halayya da xabi'a da kuma zamantakewa da tattalin arziqi na mutane.

3.4.2 Mutanen Kan Titi

Mutane jam'i ne na kalmar mutum da take nufin halittar Ubangiji mai hankali da tunani da fasaha, mai tafiya a kan qafafuwa biyu (Qamusun Hausa, 2006:354). Ke nan, mutane su ne halittar Ubangiji masu hankali da tunani da fasaha, masu tafiya a kan qafafuwansu waxanda suke rayuwa a duniya suke kuma gudanar da harkokin rayuwar ta yau da kullun. Mutanen kan titi na nufin waxannan halittun ubangiji masu hankali da tunani da fasaha, masu tafiya a kan qafafuwa

biyu da suke gudanar da harkokin rayuwarsu. Harkokin rayuwa na xaukar ma'anar hanyar da suka zava don neman abinci ko taro da kwabo.

A Zariya da Sakkwato da kuma Kano akwai qabilu mabambanta, da suke zaune waxanda suke gudanar da harkokin rayuwarsu ta yau da kullum kamar yadda kowa da kowa yake tafiyar da rayuwarsa ba tare da wata tsangwama ba. Daga cikinsu akwai, Yarbawa da Inyamurai da Katafawa da Nufawa da Ibira da Barebari da Tibi da Idoma da makamantarsu. Waxannan qabilu na gudanar da harkokinsu ta hanyar yin sana'o'i daban-daban da burin samun taro da kwabo. Akwai kuma sana'o'i mabambanta da mutane suke yi don neman abin da za su biya buqatar kai.

Mutane iri-iri ne kowane mutun akwai shi ko akwai ta da yanayin rayuwa, wasu na yin abubuwan da suka dace; yayin da wasu kuwa abin ba a cewa komai. Wannan ya haifar da mutane na gari da kuma lalatattun da suke rayuwa a doron qasa.

Na gari abu mai kyau, wanda kowa ke son abin. Mutane iri-iri ne ta fuskar xabi'a akwai na gari mai kyau wanda kowa yake so yake kuma burin ya zama ko a danganta shi da wannan mutum.

Karin magana na cewa ….

> "*Na gari na kowa' wadda ake cikasawa da cewa 'Mugu sai mai shi'***,** *kuma karin magana nau'i ne na adabin baka. Adabi kuma hikima ce da ta qunsu cikin harshe; shi kuwa harshe maqunsar tunani ne ko saqo ko ilimi. Na gari mutumin kirki, maisauqin kai, ga fara'a da son mutane*" (Muhammad, 1997).

Mutumin kirki kamar yadda Kirk-Greene (1974:16) ya bayyana mutum ne mai hali da gaskiya da amana da karamci da haquri da hankali da kunya da ladabi da mutumci da kuma kirki.

> *"Na gari shi ne mutumin da ke zaman lafiya da kowa kuma kowa na sonsa. Kamar yadda karin maganar Hausa ke nuna wa ; Na gari na kowa, Mugu sai mai shi. Haka kuma kowa ya yi na gari don kansa kuma na gari shi ke sai da kansa. Zama mutum na gari ya haxa da biyayya da alheri da mutumci da sauransu*". (Amin, 2002:264-265).

Tabbas a cikin mutanen da suke rayuwa akwai waxanda suke na gari ne domin kuwa sun fito kan titi ne da manufar neman abin da za su rufawa kan su asiri a rayuwar duniya. Har wayau, akwai malamai waxanda suke da ilimi na addini kuma suna amfani da ilimin nasu wajen gudanar da harkokin rayuwar tasu da ma masu ilimin boko.

Latatattu jam'i ne na kalmar lalatacce. Lalatacce na da ma'anar hali marar kyau, fasiqanci, shegantaka ko shaqiyanci. (Qamusun Hausa, 2006:300). Lalatacce kishiyar na gari na kowa ne, wannan ne ma ya sa ake cikashe wannan karin magana da 'mugu sai mai shi'. Tabbas ko tantama babu idan an yi maganar mutane lalatattu to akwai su a kan titi, kusan ma a iya cewa, ai nan ne ma matattararsu ko cibiyarsu a saboda kasancewar wurin ka zo na zo. Akwai mutanen da su sun fito kan titin ne da manufar aikata miyagun abubuwa ko aikata laifuka irin su sace-sace da shaye-shayen miyagun qwayoyi, wanda daga qarshe kan haifar da aikata kowane irin laifi da xan-adam kan iya aikatawa a duniya; matuqar dai za a sami quxi a yi bushasha.

Da zarar an yi magana ko aka ce a kan titi tunanin da kan zo ran mutane shi ne, wuri ne na aikata ayyukan assha, to amma ka da fa mu manta kamar yadda na ambata a sama ba a taru an

zama xaya ba; dalili kuwa akwai waxanda ba hakan suke ba. Kuma kinaya ce aka yi don bayyana wani nau'i na Hausa da ake yi a lokacin sadarwa.

Hausawa kan ce mutum fari ne, shi ke rina kansa ya zama baqi. "Mutum dangin shirinya. "Shirinya ravi-ki-kashe". "Mutum mugun ice". (Amin, 2004 :212-213). Na kawo waxannan karin magana ne don bayyana yadda Hausawa ke kallon mutum lalatacce ko mutane lalatattu, wato, mugu sai mai shi. Wannan ne ma ya sa ake kallon lalataccen mutum da munanan halaye tare da munanan ayyuka.

3.5 Sana'o'in Kan Titi

A san mutum a san cinikinsa. An fara da wannan kirari ne dangane da ire-iren sana'o'in da ake yi ko ake samu a kan titi. Sana'a na nufin aikin da mutum yake yi don samun abinci. (Qamusun Hausa, 2006:387). Sana'a na nufin hanya ko wani aiki da mutum xaya ko wasu mutane suke bi domin samun abin masarufi, wato yin duk wani abu da zai samar wa mutum kuxi don saka wa a aljihu wadda al'umma ko al'ada ta aminta da ita ko kuma wadda al'umma ba ta yadda ba amma wasu daga cikin al'ummar na yi a rayuwa. Misali sace-sace da sayar abubuwar da kan sa maye da makamantansu.

3.5.1 Masu Motocin Haya

Akwai masu motoci da suke amfani da motocinsu a kan titi a matsayin hanyar sana'arsu da suke yi don gudanar da harkokin rayuwarsu na yau da gobe. Sana'ar tuqi sana'a ce da wasu mutane daga cikin al'ummar Hausawa ke yi domin neman abin biyan buqatar rayuwa.

> *"Sana'ar tuqa mota ta samu a qasar Hausa a bunqasar qere-qere a duniya, Hausawan farko sun fara tuqa manyan motoci na kasuwanci ba na hukuma ba. Ga dukkan alamu Yarbawa da Nufawa suka zo da sana'ar tuqi a qasar Hausa. A taqaice, sai bayan da sana'ar tuqi ta samu karvuwa aka fara buxe tashar mota a arewacin Nijeriya"* (Bunza, 2005:9).

Tasha muhimmin wuri ne ga harkokin sana'ar tuqin mota ta haya. Tasha na da ma'anar wurin tsayuwar mota ko jirgin sama ko ta ruwa, don sauke ko xaukar fasinja da kaya. Tasha wuri ne da ya qunshi matafiya fasinjoji da 'yan kamasho da direbobi da sauran masu abin sayarwa. Tasha wuri ne na hada-hadar mutane maza da mata, wuri ne inda mutane suke zuwa domin yin tafiya daga wannan wuri zuwa wancan.

> *"A qa'idar tuqin Hausawa za a ba direba mota ya nemo kuxi da ita a biya shi ladarsa. Idan a ka ba shi motar, shi ke da ikon nemo wa motarsa yaro watau (karen mota). Wasu kan yi qa'idar cewa, idan motar ta biya kuxinta sai a yi wa motar kuxi, a kasa kuxi gida uku. A wata qa'idar kuwa, sati duk za a qayyade abin da ake son ya kawo na kuxi. Idan aka yi qa'ida da direba ya sava sai a karve motarsa a bar shi a banza. Ga al'ada a kan aza wa direba wasu dokoki na cewa, idan ya sava su za a karve mota. Akwai kuma tsarin haya-facezi"* (Bunza, 2005:9).

Kamasho kalma ce ta Ingilishi da ke nufin '*commission*' wadda aka Hausantar da ita zuwa kamasho. 'Yan kamasho rukuni ne na mutane da suka xauki sana'ar tsayawa a wuraren da motocin haya suke tsayawa, a tasha ko a wata babbar mahaxa da sukan riqa kiran fasinjoji domin su shiga motar haya; daga qarshe sai a ba su wani abin hassafi. 'Yan kamasho ba direbobi ba ne sai dai masu sana'a ne tare da masu motocin haya.

Kamasho sana'a ce wadda ake samun tsofaffi da matasa maza suke yi ana samunsu a tashoshin mota, da ma duk wata mahaxa da mutane suke yawan haxuwa a gefe ko kuma a kan titi, a cikinsu akwai waxanda asalinsu Hausawa ne da kuma waxansu qabilun da ba Hausawa ba. Ana yin sana'ar kamasho a tashoshin mota da kuma duk wata babbar mahaxa ko wajen tsayawar motoci, wato madakata.

3.5.1.1 'Yan Bas (Bus)

Bas kalma ce ta Ingilishi da aka fassara ko a ka Hausantar da ita da **BAS** da take nufin motar da aka ware ta domin yin haya wadda take da kujerun zama guda goma ko kuma mai 18 ko 22. Akwai motocin haya na bas kamar C20 da Hayis da Urban da makamantansu.

Xan bas shi ne mutumin da ya mayar da hanyar neman abincinsa ta tuqin irin waxannan motoci, yana yin zirga-zirga da jama'a daga wannan unguwa zuwa wancan unguwa ko kuma daga wannan gari zuwa wancan gari. Xan bas tare yake da yaronsa wanda ake kira yaron mota ko karen mota, shi ne wanda kan riqa taimakon direba wajen kiran fasinja musamman ma a tsakanin masu zirga-zirga a cikin gari. Haka kuma, ana samu a tsakanin masu zirga-zirga daga

wannan gari zuwa wancan gari. Maza ne aka sansu da sana'ar tuqin bas da ma yin karen mota a Zariya da Kano to amma a Sakkwato babu 'yan bas kamar Zariya da Kano.

3.5.1.2 'Yan Tasi

Tasi kalma ce ta Ingilishii '*taxi*' da take nufin qaramar mota da ake amfani da ita domin yin haya a kan titi wajen neman nera da kwabo. A Zariya, mafi yawan motocin tasi a yau ba su da fenti na musamman da yake rarrabe su da sauran motoci qanana, sai dai da zarar an gan su suna da almomin da suke bayyana su. Motoci ne qanana marasa tsada kamar *Golf* da *Toyota* da *Datsun* da *Peugeot* da *Mazda* da *Passat* da makamantarsu. An fi samun motocin tasi daga Samaru zuwa Kongo daga Kongo zuwa Gaskiya da xan magaji da Park road zuwa Kongo da kuma Kofar Doka zuwa xan magaji da Wusasa. Sannan kotun 'yan azara zuwa hanyar Soba da kuma kofar doka zuwa hanyar Soba. Xan tasi kuwa shi ne mutumin da ya mayar da hanyar zirga-zirga da mota qarama a matsayin sana'arsa da yake neman taro da kwabo wadda yake xaukar fasinjoji a ciki. A Kano kuwa kusan a ce babu wurin da xan tasi ba ya shiga ko ba a samunsa, a Sakkwato an fi yin haya da babura duk da yake akwai 'yan tasi.

3.5.2 ‘Yan A-cava (Masu Haya da Babura)

Kalmar babura jam’i ne na babur. Babur na nufin abin hawa mai qafa biyu mai aiki da inji da kai na riqewa, yana da gudu sosai, amma bai kai na mota ba (Qamusun Hausa, 2006:26). Wasu kan kira mai wannan sana’a da suna xan kabu-kabu da xan goyin ko xan ayisfires. Wannan harka sana’a ce kamar yadda wannan masani ke faxa:

> *”Wasu na kiran sana’ar haya da babura da suna a-cava. Sana’ar a-cava, sana’a ce da ta jivanci haya da babura. Wannan kalma ta samo asali ne daga irin halayyar masu hayar babura inda suke xauko zunduma-zunduman ‘yan mata goyo biyu. Bisa wannan dalili idan wani abokin sana’arsu ya gan shi sai ya ce da wanda ya xauko matan lalle ka cava”.* (Fagge, 2004:125).

Yayin da wasu suke ganin a’a ai a dalilin kai komo da suke yi ne a lokacin gudanar da sana’ar shi ya haifar da wannan suna. Wasu kan kira mai wannan sana’a da suna xan a-cava ko xan-kabu-kabu da wanda yake nufin mutumin da yake xaukar mutane da babur, ko da mota wadda ba ta haya ba ana biyansa. Amma a Sakkwato sunan xan a-cava xan kabu-kabu. ‘Yan a-cava sun kasu kashi uku dangane da gudanar da sana’arsu. Kamar haka:

I. ‘Yan awizo, wannan rukuni ne na ‘yan a-cava da kullum za a ga babur xinsu tsaf-tsaf, kana cike da kwalliya da abubuwa kamar hotuna da faya-fayen sidi ; suna tafiya suna goge tayoyin mashin da tsumma kuma suna karkacewa a kan mashin xin.

II. ‘Yan arubta, su ne waxanda kullum a cikin gudu suke ko da kuwa akwai cinkoso sai sun san yadda suka kukkutsa da kuma kurkurxawa tsakanin motocin da suke wucewa ; don kawai su ga sun wuce.

III. ‘Yan farar hula, su ne masu bin qa’idojin tuqi tafiya cikin natsuwa masu qoqarin bin qa’idojin hanya daidai gwargwado ; mafi yawansu dattijai ne.

A qasar Hausa maza ne matasa da tsofaffi masu aure da marasa aure suke gudanar da wannan sana’a ta a-cava.

3.6 Naxewa

A wannan babi an yi qoqarin bayyana karin harshe da majiya harshe xaya da kuma dangantakar harshe da al'umma a mahangar masana. Kasancewan babin na da taken mutanen kan titi da sana'o'insu, wannan ne ya sa a ka tsunduma wajen kawo ma'anar kan titi da mutanen kan titi da sana'o'i daban-daban da ake da su. An kuma bayyana yadda mutanen kan titi suke da ya haifar da mutane na gari da kuma lalatattu, hakan ke yin jagoranci wajen qirqirar harshen da za a yi sadarwa da shi a lokacin sadarwa. Bayanan sana'o'in da aka yi sun haxa da masu haya da abubuwan hawa da suka qunshi masu bas da 'yan tasi da kuma 'yan a-cava da ire-irensu daga nan sai aka naxe babin.

Babi Na Huxu

Sigogin Hausar Kan Titi

4.1 Gabatarwa.

Wannan babi, ya tsunduma ne wajen bayyana da kuma warware ma'anar Hausar kan Titi wadda wasu rukunonin Hausawa masu sana'o'i ko masu aikata laifi suke yi da niyyar cimma burin sadarwa a tsakaninsu. Wannan nau'i na Hausa, ana yi ne ta hanyar voye ko saye wasu muhimman saqwanni, ana faxaxa ma'ana ko tattare ma'ana wuri xaya da manufar kawar da hankali ko tunanin waxanda ba a son su fahimci abin da ake nufi. Akwai Hausar masu haya da ta haxa da masu motocin haya da bas da masu haya da babura (‘yan a-cava). Sai Hausar masu sayar da sayen kayan sa maye. Wato Hausar ‘yan giya da ‘yan wiwi da ‘yan sholisho ko shava da ‘yan qwaya da kuma Hausar ‘yan kodin da suke kira zumar kemist. An yi warwarar Hausar kan titi ta fuskoki biyu ne. Abin nufi kalmomi da kuma jimloli da ake amfani da su a Hausar kan titi, musamman daga vangaren masu haya da bas. Jimlolin da ake samu sauqaqa ne; an kuma yi qoqarin bayyana yadda zubi da tsarin wasu jimloli suke da azuzuwan aikatau da ake samu. An nazarci yadda Hausar ‘yan a-cava da Hausar ‘yan wiwi suke a garin Kano da Zariya da kuma Sakkwato.

4.2 **Hausar Kan Titi**

Hausar Kan Titi kinaya ce. Bayero (1997:145) ya ba da mana'ar kinaya da cewa " salon da a kan kira mutum ko wani abu da sunan wani abu daban da ba shi ba". Yayin da Qamusun Hausa (2006:245) kinaya ita ce "Saye ko voye ma'ana ko siffar abu saboda wani dalili. Kissa ko yaudara ko alkunya". Hausar Kan Titi kinaya ce da aka yi wa kalmar titi da ke nuni da wani nau'i na Hausa da ake samu a tsakanin rukunin masu gudanar da harkokin rayuwarsu na yau da kullum a kan titi ko ba a kan titi ba. Irin wannan Hausa masu sana'o'i da masu aikata laifi ko shaye-shaye su na yin ta a ko'ina, abin nufi a kan titi ko a kasuwa ko a mashaya ko a makaranta ko a fada kai har ma a masallaci a wasu lokuta. Abin lura da wannan nau'i na Hausa shi ne batu ne na muhalli da kuma buri ko manufar sadarwa a rubuce ko a magance, ba batu ba ne na rashin xa'a da rashin kunya da rashin sanin yakamata ba. Karin harshe ne da ake yi a lokacin sadarwa don cimma buri ko manufar sadarwa ta hanyar qirqirar kalmomi da ma jimloli da kan voye ko saye ko sakaya maganar ta xauki wata ma'ana wadda ba ita ce a sarari ko a zahiri ba. Amma tana da wata ma'ana daban da ake nufi.

Hausar Kan Titi nau'i ce ta Hausa da wasu rukunin Hausawa kan yi amfani da karin harshen Hausa don sadarwa. Kamar yadda Babanzara (2006) ya bayyana karin harshen rukuni a matsayin zaurance. Xantumbishi (2003 da 2011) ya kira karin harshen rukuni a matsayin sara "*Slang"*. Bugu da qari, Wurma (2002) ya yi magana a kan faxaxa ma'ana ko taqaita ma'ana, inda ya bayyana shi a matsayin wani fanni ne mai nuna ci gaban harshe.

Ke nan, Hausar kan Titi kinaya ce da ke bayyana wani nau'i na Hausa da ake amfani da karin harshen rukuni da wasu mutane suke yi don sadarwa da niyyar saye ko voye wani ko wasu muhimman saqwanni da suka danganci harkokin rayuwarsu na yau da kullum; ta hanyar sana'a ko ta hanyar aikata laifi ko abin ashsha . Ana yin wannan karin harshe ne don a vad da bami ko a cuci ko a yaudari mutum, wanda wannan rukuni na mutane ko majiya harshe xaya ke yi ta yadda sai xan hannu ne kawai kan gane ko ya fahimci ma'anar abin da aka faxa ko ake nufi.

Wannan nau'i na Hausa kan tafi da zamani domin kuwa yawancin kalmomin da ma jimloli na samuwa ne daga tsofaffin da aka sani da, da kuma waxanda ake amfani da su a yau duk da yake ma'anar da ake nufi daban da ma'anar da aka saba. Ke nan, ma'anar da ake nufi na tasowa ne daga waxannan kalmomi sai a samar ko a qirqiri sabuwar ma'ana. Kasancewar harshe rayayyen abu da kan rayu ya kuma mutu.

Wannan bincike ya kalli Hausar kan titi ta fuskoki biyu:

i. Hausar kan titi na 'Yan haya.

ii. Hausar kan titi na masu sayar da sayen kayan Maye. (Hausar Mashaya)

4.3 Hausar ‘Yan Haya.

4.3.1 Hausar ‘Yan Bas

Masu haya da motoci sun kasu kashi daban-daban, amma wannan bincike ya togance ne a kan masu haya da bas.

Hausar masu motocin haya da bas wani nau’i ne na Hausa da ya kevanta ga masu sana’ar tuqin mota ta bas, sukan yi amfani da kalmomin harshe da ma jimloli don bayyana wani hali ko yanayi da suka tsinci kawunansu a ciki lokacin gudanar da sana’ar su.

> *“Ga al’ada, idan an ba direba mota wadda zai riqa tuqawa a kan qayyade masa kuxin aiki da mota da zai riqa kawo wa a wani qayyadajjen lokaci, da kuma shimfixa wasu dokoki. Sava wa waxannan dokoki kan iya haifar da a karve motar, wasu lokuta magabta ne masu son a karve motar suke kawo qarar direba; wasu lokuta kuwa ‘yan uwansa direbobi ne da dai sauransu”* (Bunza, 2005).

A na amfani da kalmomi da ma jimloli waxanda ake furta wa da baki kowa zai ji abin da aka furta, to amma inda gizo ke saqa ba kowa ne kan san ma’anar abin da aka furtan ba sai xan hannu. Waxannan abubuwa kan bayyana halin da direba ko yaron mota ya tsinci kansa ne tsakaninsa da fasinjoji da motar ita kanta, da ma jami’an tsaro da sauran mutane a lokacin da ake amfani da motar, kodai na farin ciki ko kuma akasin haka. Wannan ya haifar da samar ko qirqirar wasu kalmomi da ma jimloli da a kan yi wa kinaya don dai a huce takaici ko kuma a bayyana samun abin da aka fito nema.

Kalmomi: A nan masu Hausar kan yi amfani da kalmomi ne waxanda a sarari ga ma'anar da kalmar ke da ita, amma su kuma ga ma'anar da suke nufi.

Misali:

Lamba	**Kalma**	**Ma'ana (A)**	**Ma'ana (B)**
1	Bùloô nee	Fasinjar da ba za a karvi kuxinsa ba.	Abin gini
2	Gyaaraa	Qari a bisa wajen saukar fasinja	Kwaskwarima
3	Kwaˆal/ ma'a`ika`acii	Xan sanda	Mai aiki
4	Saa-wutaa	Direba ya yi gudu	Ta ka ta
5	Sai òogaa	Gaisuwa	Direba mai tuqi
6	Zàabii	Fasinjan da ba sa shiga tasha	Tsuntsu
7	Zàlaamàa	Handama	Zalama

Kalmar zalama ba ta da wata ma'ana a Hausa sai dai ma'anar da suke nufi ita ce handama da babakere da yawan son kai. Haka kalmar Kwal da ke da ma'anar xan sanda.

A kalma mai lamba 1 da 3 da 7 an yi qirqira.

A kalma mai lamba 2 da 4 da 6 an yi saye.

A kalma mai lamba 5 an yi aro da inglishi.

Akwai wasu jimloli da masu tuqin bas suke amfani da su. 'Yan bas na yin Hausarsu don su kawar da tunanin masu sauraren su, ta yadda su ne kawai ko waxanda aka yi wa bayani kan fahimci ma'anar da suke nufi.

Misali:

Lamba	**Jimla**	**Ma'ana (A)**	**Ma'ana (B)**
8	Ájìyee ta gàbansà	A yi fakin a gaban wata mota	Shige gabansa
9	Anàa xan samunsà à nân	Ana samun fasinja kodayaushe	Suna ne
10	Álhajì/ Malàn gyàaraa	Wato namiji ya matsa	Salon a gyara zama

11	Xagà qafà	Direba ya tsaya wani ya shige	Alfarma
12	Xàukoo shì	A wuce wani direba akan titi	A ba da alfarma
13	Fàsà wannàn	Neman canjin kuxi	Hudawa
14	Gòoyaa ta	A ravaa mota a wani wuri	
15	Gàa naamù nan	Idon sani	Ga wani abu nan namu
16	Hajìya/ màatar maalàm gyàaraa	Wato mace ta matsa	A matsa
17	Ìnaa nèe	Ina za ka?	Wane wuri ne?
18	Kà dakèe	Ka yii hakuurii	Ka manta
19	Kuxin gwamnatìi	Kuxin lodiin farko na	Kuxin gwamnati

		mota	
20	Kù kulàa dà àljìihuu	Xan sane ya shigo motar	Hankali da aljihu
21	Mù jee samàa	Mu tafi	Ja mu je
22	Mun kashèe gàrii	An samu kuxi	An kashe gari
23	Rìqee masà bambàa	A hana wata mota wuce wa	
24	Sàkaa ta à nân	A ajiye mota a wuri na musamman	Saka wani abu a wani wuri
25	Saa kâii	Direba ya wuce babu mota mai zuwa	Sa kai
26	Taa kaamà loojìn	Mota ta lalace akan hanya	Kama wajen kwana
27	Tuwoo xayaa naamàa xayaa	Xan tasi	Tuwo da nama
28			

	Yìi matàa lambàa	A gogi wata mota	Alama

Zubi da Tsarin Jimlolin ta Fuskar Nahawu

Jimla mai lamba

8. J_= YS + YA

YS = ~~O~~

YA = G.A

G.A = Aik + Karvau + Byn

Aik = Ajiye (aikatau xan aji 4)

Karvau = W.S

W.S = ta

Byn = gabansa

9. J_= YS + YA

YS = ~~O~~

YA = Aik + Tsig + Byn

Aik = Ana

Tsig = xan

Byn = samunsa a nan

10. J = YS + YA

YS + YA

YS = Sft 1 + K2 + Sft3

Sft1 = ~~O~~

K2 = SN

SN = Alhaji / Malan

Sft3 = ~~O~~

YA = G.A

G.A = Aik

Aik = gyaara

11. J_= YS + YA

YS = ~~O~~

YA = G.A

G.A = Aik + Karbau

Aik = Xaga

Karvau = qafa

12. J_= YS + YA

YS = ~~O~~

YA = G.A

G. A = Aik + Karvau

Aik = Xauko (aikatau xan aji 6).

Karvau = W. S

W.S = shi

Jimla umurtau

13. J_= YS + YA

YS = ~~O~~

YA = G.A

G.A = Aik + Nunau

Aik = fasa

Nunau = wannan

14. J_= YS + YA

YS = ~~O~~

YA = G.A

G.A = LS + LL + Aik + Karvau

LS = ~~O~~

LL = ~~O~~

Aik = Goyaa

Karvau = W.S

W.S = ta

15. J_= YS + YA

YS = ~~O~~

YA = G.A

G.A = LS + LL + Aik + Karvau + Byn

LS = ~~O~~

LL = ~~O~~

Aik = Ga

Karvau = Mallaka

Mallaka = namu

Byn = nan

Jimla bayanau

22. J_= YS + YA

YS = ~~O~~

YA= G.A

G.A = LS + LL + Aik + Karvau

LS = mun

LL = ~~O~~

Aik = kashee (aikatau xan aji 4)

Karvau = gari.

23. J_= YS + YA

YS = ~~O~~

YA = G.A

G.A = Aik + Karvau

Aik = Riqe

Karvau = masa bamba

25. J = YS + YA

YS = ~~O~~

YA = WS + Aik + Karvau

WS = ~~O~~

Aik = Sa

Karvau = kai

Jimla umurtau.

26. J = YS + YA

YS = ~~O~~

YA + YS

Y.A = G.A

G.A = LS + LL + Aik + Byn

LS = Ta

LL = a

Aik = kaama (aikatau xan aji 1)

Byn = lojin

28. J = YS + YA

YS = ~~Ɵ~~

YA = G.A

G.A = Aik + Karvau

Aik = Yi

Karvau = mata lamba

Jimla umurau.

Akwai abin lura a nan, duka waxannan jimloli na da ma'anoni biyu. Ma'ana ta A ita ce ma'ana ta yau da kullum da aka saba, yayin da ma'ana ta B ke xauke da sabuwar ma'ana ta musamman da aka yi wa kinaya. Yawancin waxannan jimloli sauqaqa ne ba su da yankin suna sai yankin aiki kawai, sannan masu Hausar sun fi amfani da jimloli umurtau. Ana samun qirqira da aro da fassara da a wasu lokuta da a kan yi wa kinaya da manufar kawar da ma'ana ta asali da aka sani yau da kullum.

4.3.2 Hausar ‘Yan A-Cava

Masu haya da babura ko ‘yan a-cava ko ‘yan kabu-kabu na da wani nau’i na Hausa da suka qirqira suke amfani da shi a lokacin gudanar da harkokin sana’arsu ta haya da babura. Wannan ya haifar da samar da wasu kalmomi da ma jimloli da kan bayyana hali ko yanayin da aka tsinci kai a lokacin gudanar da sana’ar ta a-cava. Hausar ‘yan a-cava kan bayyana da kuma siffanta baburan ne da fasinjoji da sukan su ‘yan a-cavan da ma duk wasu waxanda aka ci karo da su a lokacin gudanar da sana’ar. Hakan ne ya haifar da qirqira da aro da ma kinaya da ake samu a cikin Hausar tasu, ta yadda za su ce abu kaza to amma ba fa wannan abu suke nufi ba. Manufa sun samar da wani nau’i na Hausa don ganin an kawar da fahimtar wanda ko waxanda ba xan ko ‘yan hannu ba ne.

A Hausar kan titi na ‘yan a-cava ana samun kalmomi da ma jimloli da suke amfani da su a lokacin sadarwa .

Kalmomi a Hausar ‘Yan a-cava:

Lamba	**Kalma**	**Ma’ana (A)**	**Ma’ana (B)**
1	Ábajèe	Karikitan jikin babur	Warwatsawa
2	Baabaa	Salon gaisuwa ne	Baba
3	Bâlbeelàa	Wanda ba ya biyan kuxi	Tsuntsu

4	Bookòo hàrâm	Honda mashin	Sunan wata qungiya ce
5	Buksà/ râi banzaa	Sunan mashin ne	----------
6	Bàqàdaamuushèe	Sojan haya	Soko
7	Bùuxè wutaa	A tafi da sauri	A buxe wuta
8	Vaatà-hazoo	Babur mai hayaqin tsiya	Dusar sanyi
9	Dàashiì	Shida	----------
10	Dookìinaa	Mashin xina	Dabba
11	Xiihù	Huxu	Suna ne
12	Gàndaa	Macen da take tuqin mota	Wani nau'i na nama
13	Gàuraakàa	Baqauye	Tsuntsu

14	Gidaa nèe	Jin daxi	Gida ne
15	Hannun qwaryaa	A ba wani mashin ya yi aiki da ita	Hannun kwarya
16	Hayà	Yin amfani da babur na xan kabu-kabu, a biya bayan qayyadajjen lokaci	----------
17	Jigìdaa	Babur mai ba da matsala kullum	Harsashin bindiga
18	Jàakii	Babban babur	Suna dabba
19	Kaariigoo	Yarinya mai hawa babur da ba ta da kuxi	Xauka ka tafi
20	Karfà	Yarinya mai hawa babur da ba ta da kuxi	Karfa
21	Kâi xayaa	Dubu xaya # 1000	Kan ice xaya

22	Kòoraa	Yawon neman fasinja	Wani cuta da ake samu a kan mutum
23	Kwaxxò	Qaramin babur	Sunan wani dabba
24	Kwaayàawaa	Bakwai	Kaya
25	Kancal	Mai vata harka	Shisshigi
26	Kyànkyasòo	Sabuwar mashin	Kwaro
27	Làwincìs	Lafiya lau	Lawincis
28	Laawùs	Salon gaisuwa (ya kake ?)	Lawus
29	Maa	Goma	----------
30	Mastà	Salon gaisuwa ne	----------
31	Malàucinkà	Basarwa	Kaucewa

32	Mutuwàare	Mataccen babur	Gurin ajiyar gawa
33	Màaji	Kuxi	----
34	Sabôn-kaamu	Baqo a cikin sana’ar	Sabon kamu wa
35	Sòojaa	Wanda ba shi da mashin	Soja
36	Soolò	Yawoo ba fasinja	?
37	Shatàa	Yin jinga da xan kabu-kabu ya yi ta yawace-yawace da mutum	Sunan wani mawaqi
38	Sùuwìs	Ya abubuwa ?	Suwis
39	Taa tàagujee	Tsohun mashin	Suna ne
40	Taa kûllee	Ba fasinja	Kullewar wani abu

41	Tuu fàakin	Mutane biyu a mashin xaya	Tu fakin
42	Tanìimu bàqìi	Xan qauye wanda baya iya biyan kuxin mashin	Suna ne da kala
43	Tsàama	Sabon mashin	Tsama
44	Tsuulà	Tsohun mashin	Tsigalau
45	Tsìini	Xan sanda	Dafi
46	Tsînka	‘Yan sanda	Tsinkewa
47	Kwaskwàa	Xan a-cavan da bai kawo balas	
48	Wincìs	Lafiya lau	Wincis
49	Yuu	Biyu	Danqo (fari)
50	‘Yar rakàa	Budurwar da za a yi harka	Wacce za a raka

51	Zan-zam	Gyararre	Lafiyayye
52	Zaazuu	Shataa	Suna ne

Akwai kalmomin da ba su da wata ma'ana kuma ba su a Hausa, amma 'yan a-cava sun samar da su kuma suka ba su ma'ana. Haka kuma akwai waxanda 'yan kabu-kabu ne ke amfani da su, manufa Sakkwatawa, kalmomi kamar jaki da soka su da haya da kora da kwaxxo da tava-ka-lasa da makamantansu.

Kalmomin Qirqira/ Saye ko Kinaya

A kalma mai lamba ta 1-8 da 9-18 da 21- 30 da 32-41 da kuma 43-52.

Kalmomin Fassara/ Aro

A kalma mai lamba ta 7 da 20 da 31 da kuma 42.

A misalai masu lamba 1 da 8 da 9 da 11 da 13 da 17 da 26 da 29 da 32 da 36 da 39 da 44-47 da 49 da kuma 52 (Fagge, 2004) ya kawo su a cikin aikinsa.

Ba a samun abu xaya a duk garuruwan da aka nazarci Hausar 'yan a-cava, sai dai a kan sami kamanceceniya a karin harshen a wasu wurare inda za ka ji ana amfani da kalma kaza a wannan gari haka ma a wancan gari.

Jimloli a Hausar 'Yan A-cava.

Akwai wasu lafuza na jimloli da 'yan a-cava suke amfani da su na karin magana da kirari waxanda suka kevanta da su kawai. Ba kowa kan fahimci ma'anar ba sai xan hannu ko wanda aka sanar da shi. 'Yan a-cava na amfani da sauqaqan jimloli masu qunshe da karin magana ko kirari, waxanda suke bayyana wani abu na musamman da su ne suka san hakan. Manufa akwai qirqira da ke xauke da kinaya a cikin ire-iren waxannan zantuttuka. Misali:

Shiga na duba ma. Wannan jimla na da ma'ana biyu.

A. shiga babu mai zuwa

B. Xan a-cava mai ganganci

J = YS + YA

YS = ~~O~~

YA = G.A

G.A = Aik + Ws + Aik + Karvau

Aik = Shiga

WS = na

Aik = duba

Karvau = ma

Aha! Ladan ka fi liman niyya.

A. Xan A-cava mai gaggawa

B. Xan A-cava da baya bin doka a lokacin tuqi

J = YS + YA

YS = Amsa-kama + suna

Amsa-kama = Aha !

Suna = Ladan

YA = G.A

G.A = Ws + Aik + Karvau

WS = ka

Aik = fi

Karvau = Liman niyya.

Su qare.

A. Wasu mutane ko wasu abubuwa su qare

B. Xan a-cava da ya fi son ya xauki fasinjoji mata kawai

J = YS + YA

YS = ~~O~~

YA = G.A

G.A = WS + Aik

WS = Su

Aik = qare.

Xauki kare, mage sai an ba da kuxi.

A. Xauki kare mage sai an biya kuxi

B. Xan a-cava da ke xaukar ‘yan mata da manufar ya yi lalata da su.

J = YS + YA

YS = ~~O~~

YA = G.A

G.A = Aik + Suna + Byn + Aik + Karvau

Aik = Xauki

Suna = kare

Byn = mage sai an

Aik = bada

Karvau = SN

SN = kuxi.

Xan a-cava rigarka ba ta salla.

A. Xan a-cava da kayansa ba su da tsarki

B. Xan a-cava da babu tsarki tare da shi

J = YS + YA

YS = SN + SN + Mallaka + Korewa

SN = Xan a-cava

SN = raga

Mallaka = rka

Korewa = ba

YA = G.A

G.A = WS + Aik

WS = ta

Aik = salla

Xan bakin ciki.

A. Mutum mai baqin rai

B. Xan kabu-kabu mai aiki tsawon awa ashirin da huxu (24 hrs)

J = YS + YA

YS = Tsig + Sifa + Suna

Tsig = Xan

Sifa = bakin

Suna = ciki

Kago na Alu ga gudu ga kaye.

A. Kago na Alu ga gudu ga kaye

B. Babur qirar kago wanda gwamnatin jihar Sakkwato ta rabawa ma'aikata

J = YS + YA

YS = Suna + WS + Suna

Suna = Kago

WS = na

Suna = Alu

YA = G.A

G.A = Aik + Byn

Aik = ga gudu

Byn = ga kaye.

Gari ya qiya.

A. Gari ya qi

B. Rashin ciniki ko fasinja a gari

J = YS + YA

YS = K2

K2 = Suna

Suna = Gari

YA = G.A

G.A = LS + LL + Aik

LS = ya

LL = a

Aik = qiya.

Jiya ba yau ba.

A. Jiya ba yau ba

B. Salo ne bayya damuwa da Xan a-cava ke yi lokacin da ya kalli babur xinsa.

J = YS + YA

YS = Suna + Korewa + suna + Korewa

Suna = Jiya

Korewa = ba

Suna = yau

Korewa = ba.

Kowace jimla na da ma'ana biyu, ma'ana ta A ma'ana ce ta yau da kullum yayin da ma'ana ta B ita ce sabuwar ma'ana. Haka kuma akwai wasu jimloli da 'yan kabu-kabu ne ke amfani da su, manufa Sakkwatawa a jimla mai cewa (Gari ya qiya) da (Jiya ba yau ba) 'yan a-cava Kanawa ke amfani da wannan jimla.

Dangane da zubi da tsarin jimlolin ta fuskar nahawu kuwa, yawancin jimlolin ba su da yankin suna yankin aiki ne suka fi xauke da shi.

4.4 Hausar masu Sayar da Sayen Kayan sa Maye

Shaye-shaye ya samo asali ne daga shan magani da mutum mara lafiya ke yi don neman waraka daga cuta ko cututtuka da suke damun mutum xin, saboda cigaba da wanzuwa a rayuwa. A al'ada likita ko ma'aikacin lafiya kan rubuta magani ga mara lafiya da zai nema ya sha bisa qa'idar da aka shimfixa don shan magani. Karya ko wuce qa'idar da aka shimfixa don shan magani ko a sha ba tare da lalurar rashin lafiya ba shi ake nufi da shaye-shaye. Shaye-shaye a fahimtar wannan bincike iri biyu ne: na gargajiya da na zamani.

I. Na gargajiya na da can wadda Hausawa suke yi kafin bayyanar abubuwar cigaban zamani.

II. Na zamani wadda Hausawa suka samu bayan bayyanar nasara ta hanyar shan magunguna da abubuwan da suka kawo masu sa maye.

A kowace al'umma ana samun wasu mutane ko rukuni na mutane masu shaye-shaye waxanda suke shan abubuwan da kan sa maye. Haka wannan lamari yake a cikin Hausawa inda ya kasance tamkar annoba ko wutar daji. A tsakanin rukunin matasa da ma tsofaffi maza da mata, masu ilimin boko da marasa ilimin boko; da marasa ilimin addini kai har wasu lokuta a kan sami masu ilimin addini a cikin wannan hali.

"Sha ba shashanci ba, wani aikin sai an shawu". Kamar yadda mashaya kan faxa. An fara da wannan batu ne don qoqarin bayyana Hausar mashaya. Mashaya dai kamar yadda aka bayyana a

baya, wasu mutane ko rukuni ne na masu shaye-shaye waxanda suke shan abubuwar da kan sa maye da manufar yin maye.

Mashaya na yin wani nau'i na lafazi, wato kalamai a cewar Gidan Dabino, (2012:31) ya ce

> *"Yan maye suna da wasu kalamai da suke yi a tsakaninsu wanda kusan su kaxai suke sanin ma'anar abubuwan da suke nufi, sai kuma wanda aka yi wa bayani ya fahimta ne kawai yake iya gane manufarsu. Yawancin wannan zaurance shi ma wata alama ce ta buguwa da gushewar hankali da rashin gaskiya da aikata laifi wanda ke da alaqa da illolin shaye-shaye".*

Ga wasu daga ciki kamar haka :

a. Za mu je dubun nahiya (wurin shan kayan maye ke nan).
b. Muna cikin dubun aiki (an shawo qwaya ke nan).
c. Mun murxe masa kai (murfin kwalbar abin da suka sha ke nan).
d. Mun hau network (kai ya xauki caji ke nan).
e. Mu je zubi (za a je shanqwaya ke nan).
f. Muna so su yi slow (ana so a yi maye ke nan).
g. Za mu qara wa sama hazo (za a sha wiwi ke nan).
h. Buguwa ma sai a can (wato buguwa sai a lahira).
i. Haxin da ba duk kai ba (a haxa qwayoyi da maganin mura iri daban-daban).
j. A sha komai (ma'ana ba su bar kowane abin maye ba).
k. Yaya ruwa? (ba za a sha ba ne yau).
l. Weza (weather) ta ba da haxin kai (yanayin gari ya yi daxi ke nan).
m. Aiki to, aiki kurum (wato in ba a sha ba a sha).

n. Akwai gem, za a fasa eriya (za aje wata matattara inda manyan gayu suke haxuwa don yin shaye-shaye). (Gidan Dabino, 2012:31).

Idan muka kalli waxannan zaurance kamar yadda ya kira su za mu ga cewa mashayan ne ke qirqirawa kawunansu, kuma kusan ya yi magana ne a kan duk ilahirin mashaya. Yanzun za a kawo Hausar mashaya ‘yan maye ta la’akari da nau’o’in kayan shaye-shayen da suke amfani da su a lokacin aiwatar da harkar ta shawuwa.

4.4.1 Hausar ‘Yan Giya

Giya na cikin rukunin kayan shaye-shaye da ake sha ta baki a lokacin sha. Giya abin sha ce da ake yi da hatsi ko alkama ko inabi wadda ake sha, a yi maye. (Qamusun Hausa, 2006:168). Ana kiran ta da suna barasa ko burkutu, akwai giyar qoqo da ta kwalba. Wato, giyar gargajiya da ta zamani. Giya nau’i ce daga cikin nau’o’in kayan shaye-shaye wadda ake sha da nufin a yi maye da mashayanta suke yi. Sunan mai shan giya xan giya ko a ce mashayin giya ko xan kwalba.

A qasar Hausa akwai waxanda suke hada-hada na saye da sayarwa da ma shan wannan abu, a cikinsu akwai Hausawa da waxanda ba Hausawa ba mazansu da matansu. Giya abar sha ce wadda take haifar da cututtuka kamar yadda masana ilimin lafiya suka tabbatar. Sai dai abin takaici hukuma ta aminta da wannan harka, kuma duk mai yi yana da ‘yancin yin hakan a saboda yana biyan kuxaxen shiga ga gwamnati.

‘Yan giya na da Hausar da suka qirqira suke amfani da ita da ta kevanta da mashayan giyan kawai, ana qirqira da aro da ma fassara da ke xauke da kinaya a cikin Hausar. Irin waxannan

kalmomi da ma jimloli na xauke da kalmomi da ma jimloli masu xauke da kinaya da kan bayyana giyar da halin da ‘yan giyar kan tsinci kawunarsu a lokacin sha da ma bayan shan ta.

Misali:

Lamba	**Kalma**	**Ma’ana (A)**	**Ma’ana (B)**
1.	Batìl/Batàleewà	Giya / shan giya	Batil
2.	Cizòn qòoqoo	Burkutu	Cizon qoqo
3.	Daidai	A na cikin maye	Abu ya yi daidai
4.	Gàarii	Yin maye	Gari
5.	Gidan màaman andìyaa	Gidan giya ne	Gidan maman Andiyana
6.	Gidan koorèn qwai	Gidan giya	Gida mai koren kwai
7.	Gìrîn batìl	Giya gulda (sunan giya)	Koriyar kwalba
8.	Hâi	An shawu ko an bugu	Hai

9.	Kat-kat	shan giya cikin sauri	Qa daddatsa abu
10.	Qoolee	Qololuwar maye	Qololuwa
11.	Qwaaxuu	Shan giya	Bugewa da wani abu
12.	Qwaaxè	Ana cikin maye	A buge wani abu
13.	Lallà	Sabon hannu	lala wani abu
14.	Mashaayaa	Gidan giya	Wajen shan ruwa
15.	Mài zaafii	Wiski (whisky) sunan giya	Abu mai zafi
16.	Mài hawàayee	Giya mai sanyi	Hawaye
17.	Ruwaa	Giya	Ruwan sama/sha
18.	Ruwan jìrii	Giya	Ruwa mai sa jiri
19.		Ana cikin maye	A rushe wani abu

	Rùshee		
20.	Ruwan bagajaa	Giya	Ruwan magani
21.	Shot-shot	Qananan kwalaban giya	Qanana
22.	Dawshìf	A sha giya ba tare da sauke kwalba ba	--------

Kalmomim da aka yi wa Saye / Qirqira

A kalma mai lamba ta 9 da 10 da 11 da 12 da 13 da 14 da 15 da 16 da 17 da 18 da 19 da kuma 20.

Kalmomin da ak yi Fassara / Aro

A kalma mai lamba ta 1 da 7 da 8 da 21 da kuma 22.

Lamba	Jimla	Ma'ana (A)	Ma'ana (B)
23	Ya bugèe	Ya na maye	Ya buge da wani abu
24	Rabà aikìi	Mai raba giya a gidan giya	Mai raba giya ke nan
25	Yaa shaa ruwaa	Yaa shaa giyaa ke nan	Ya sha ruwa na sha
26	Qwàaxoo shaa ruwaa idònkà yà buuxèe	Idan mashayin giya ya fara buguwa da giya ke nan	----------
27	Mù jee Manguu	Za a tafi gidan shan burkutu	Mu je garin Mangu
28	Yaa qoolèe	Ya bugu.	----------
29	Gàa wani xan gàrii nan	Ga wani xan giya nan	Ga wani xan gari nan
30	Yaa yi dai-dai	Ya bugu sosai.	Komai lafiya/ ya yi

31	Yaa riqoo buutàa	Ya riqo kwalbar giya ke nan.	Ya riqo buta ta ruwa
32	Yaa ruushèe	Ya bugu	Wani abu ya rushe
33	Yaa kwaaxèe	Ya bugu	Ya kwade da wani abu

Aikatau da azuzuwan da suka fi amfani da su.

Hausar ‘yan giya na xauke da azuzuwan kalmomi na wakilin suna da aikatau. Abin nufin mafiyawan jimlolin da aka nazarta na xauke da zubi da tsari kamar haka:

J = YS + YA

YS = ~~Ø~~

YA = WS + Aik + Byn.

Aikatau iri biyu ne so-karvau da qi-karvau kamar yadda muka sani. Dangane da azuzuwan aikatau ana samun azuzuwa kamar haka:

Bugee aji 4

Qoolee aji 4

Rushee aji 4

Kwaxee aji 4

Riqoo aji 6

4.4.2 Hausar 'Yan Wiwi

Wiwi na cikin rukunin kanabis da suka haxa da marijuwana da man hashish. Wiwi na da sunaye mabambanta da ake kiranta da shi a kan titi da suka haxa da Indian hemp da (Gras weed) ganyen wid da siton (stone) da Ganja. (NDLEA Drug Abuse Awareness Guide).

Wiwi xaya ne daga cikin nau'o'in kayan shaye-shaye da ake matuqar sha a wannan zamani. Wiwi ciyawa ce da ake shukawa ko ake nomawa wanda bayan girbi a kan sayar ga manyan dillalai, su kuma suke sayarwa ga masu sha. Ana naxawa ne ko molawa a takarda sannan a kunna wuta a riqa zuqa. Gwamnati ta hana sha da fatauci ko sayar da wiwi, doka ce ma duk wanda aka kama da laifin sha ko sayar wa akwai hukunci na musamman mai tsanani a kansa ko kanta. Har ma hukumar hana sha da fataucin miyagun kwayoyi gwamnati ta kafa don dai ganin an kawar da wannan annoba.

Shan wiwi kamar sauran kayan shaye-shaye abu ne da ya kasance annoba, akwai mashaya maza da mata, matasa da tsofaffi talakawa da attajirai masu ilimin addini da marasa shi da kuma masu ilimin zamani na boko da marasa shi.

Giyaxe, (2012) a hirar da BBC Hausa ta yi da shi ranar da majalisar xinkin duniya ta keve don yaqi da hana sha da safar miyagun qwayoyi ke cewa. " an fi yin noman ganyen wiwi a jihohin

kudu maso yammacin Nijeriya amma an fi shan ta a jihohin arewacin qasan nan musamman jihar Kano da Sakkwato da Katsina".

"Dole qanwar na qi", 'yan wiwi na da Hausa ta musamman da suka qirqira wa kansu suke amfani da ita domin sirrinta ko saye ma'anar kalmar ta xauki wani abu na daban, duk dai a qoqarin kawar da hankalin mutane da hukumomin hana sha da fataucin ta. Kasancewar wiwi haramtaccen abu a hukumance, wannan ya tilasta wa mashayan yin amfani da kalmomi na musamman da ma jimloli don gudanar da harkokin da suka danganci sha da saye da sayarwa na wiwi.

Ga wasu daga cikin Hausar 'yan wiwi:

Lamaba	**Kalma**	**Ma'ana (A)**	**Ma'ana (B)**
1	Àlfaa bùlàndis	Wiwin alfa	Suna ne
2	Bàasar	Manta da shi	A bar yin wani abu
3	Bâmàiyíi	Ma'aikatan hana shan miyagun kwayoyi	Suna ne
4	Bulau	Wiwi	----------
5	Buyaagii	Hayaniya	Fitina

6	Caamanyee	Wiwi	Camanye
7	Cilligaa	Qullin wiwi mai xan girma	Abu mara girma
8	Cikin aikì	Cikin maye	Ana aikata aiki
9	Diilàa	Mai sayar da wiwi	Diilaa
10	Duutìi	Shan daga	Duti
11	Xan gwamaa	Xan wiwi	Suna ne
12	Xan makarantaa	Xan wiwi	Wanda yake makaranta
13	Faasìl	Xaurin wiwi mai girma	----------
14	Farar laayàa	Qullin wiwi	Laya fara
15	Ganyee	Tabar da ba a sarrafa ba	Ganyen bishiya
16			

	Gida xayaa	Jituwa	Gidan kwana
17	Hàraawàa	Wiwi	Rauga
18	Haddà	Wajen shan wiwi	Hadda ce abu
19	Hannun rìigaa	Rashin jituwa, tsana	Sashen rigar sa wa
20	Hadaìi	Jami'an tsaro baqi	Hadarin ruwan sama
21	Hazoo	Hayaqi	Buji
22	Jan wuuyàa	Jarumi	Wuya ja ko kwala
23	Kàamaa-kàamaa	Shan wiwi	Xauka-xauka na wani abu
24	Kiilàa	Qarshen wiwi	Kila
25	Koorìyar hàraawàa	Xanyen wiwi	Ciyawa xanya
26	Kuukan kuuraa	Wiwi	Kura tayi kuka
27	Kulàawaa	'Yan sanda	Masu neman kare
28	Qàramin qwaqwalwaa	Mai shan wiwi 'yar kaxan ta sa shi ya yi	Mara fahimta sosai

		maye	
29	Qayàa	Wiwi	Qaya
30	Kwâl	Xan sanda	Wani nau'in ma'adani
31	Kwankwai	Wiwi	----------
32	Kwarkwaroo	Dan iska	Bututu
33	Màcè	Rago	Ta mata
34	Màdòobii	Wajen sayar da taba	Sunan gari
35	Màhammàn	Baqon ido	Sunan mutum
36	Mànduulàa	Xaurin wiwi	Mandula
37	Moolì	Naxa wiwi	Nade abu
38	Maagànii	Tabar wiwi	Maganin ciwo
39	Makoomaa	Wutar kunna taba	Inda za a koma }arshe
40	Maarìyaa	Wiwi	Sunan mutum
41	Maaròo	Wiwi	----------
42	Mangwaroorìi	Sunan wurin da ake sayar da wiwi	Mangwarori

43	Mazàajee	Fitacce	Jam’i na Maza
44	Sàabaràa	Wiwi	Wani magani
45	Sàalìsai	Wiwin salisai	Suna ne
46	Sauqii	Abin ci /sha	Hutawa
47	Siidis	‘ya’yan wiwi	Sidis
48	Taabàa	wiwi	Sigari
49	Taabàr àljànnuu	Wiwi	Suna ne
50	Tushèe	Bagidaje	Gindin wani abu
51	Ùsaamà	Kawo hari ko farmaki	Sunan mutum
52	Wà’ànkaràhuu	A lura	Wa’ankarahu
53	Wàgiilì	Shashasha	Sauna
54	Wàkaamàhuu	Za a kama	Wakamahu
55	Wàtseerùhuu	A gudu/ a tsere	Watserahu

56	‘Yar gùdaa	Shan daga	A ba da aron wani abu
57	Zàaboo	Matsoraci	Tsuntsu
58	Zoogalaa	Wiwi	Zogala

Kalmomin da suka kevanta ga Kano

Kalma mai lamba 19 da 26 da 34 da 52 da 54 da 55 da kuma 57

Kalmomin da suka kevanta ga Zariya

Kalma mai lamba 41 da 45 da 46

Kalmomin da suka kevanta ga Sakkwato

Kalma mai lamba 40 da 42 da 44 da 50 da 58

Kalmomin da aka yi Qirqira/ Saye ko Kinaya

A kalma mai lamba 1 da 3 – 8 da 11 da 12 da 13-16 da 18-23 da 25-36 da 38-46 da kuma 48-58.

Kalmomin da aka Fassara/ Aro

A kalma mai lamba 2 da 9-10 da 13 da 17 da 24 da 37 da 41 da kuma 47.

4.4.3 Hausar ‘Yan Shalosho (Shava)

Mashayan shava kan riqa shaqarta a kwalba ko a roba ko a tsumma wadda hakan kan haifar masu da yin maye. Mashaya ‘yan shava a saboda dalilin shavavewan da suke yi da kuma aikata wautar da suke yi ne ya sa ake kiran su da wannan suna. Domin idan an shave sukan aikata duk abin da mutum bai tava zaton za su aikata ba, haka kuma sukan ga aljannu a lokacin da suke sha.

Hukuma ta yarda da a riqa saye da sayarwa na wannan sinadari, to amma ba a yarda da a riqa sha ba, kuma akwai hukunci ga duk wanda aka kama yana shan wannan sinadari mai suna shava ko sholisho.

‘Yan sholisho su ma na da Hausar da suka qirqira kuma suke amfani da ita lokacin da suke sadarwa, da ta danganci shavar a lokacin da suke sha don kawar da hankali ko tunanin sauran mutane. Akwai qirqira da aro na kalmomi da ake wa kinaya, a cikin waxannan kalmomi da ma jimloli da ake yi ba kawai ‘yan shavan ne suke amfani da su ba. Sauran mashaya ma na amfani da su domin bayyana shavar da hali ko yanayin da suke ciki idan sun sha ko lokacin da suke shan shavar.

Wannan bincike ya gano cewa ‘yan shava ba su cika yin surutu ba idan sun nitsa cikin shava. Wannan ya sa ba a cika samun kalmomi ko jimloli na a zo a gani ba ko masu yawa ba daga bakunansu, sai dai sauran mashaya da ma waxanda ba mashayan ba na amfani da wasu kalmomi da ma jimloli don bayyana hali ko yanayin da suke samun kansu. Ma’ana su mashaya shavar. Ke nan, akwai waxanda su suke amfani da su da kansu da kuma waxanda sauran mutane da mashaya

suke amfani da su. Ana samun qirqira da aro da ake wa kinaya a cikin Hausar ‘yan shava kamar haka:

Lamba	**Kalma**	**Ma’ana (A)**	**Ma’ana (B)**
1	Bâ màganàa	Mashayin shava	Rashin Magana
2	Xan roobà	Xan shava	Daga roba
3	Xan kurmaa	Xan shava	Xan kurma
4	Elkà	Sholisho	---------
5	Gooloo	Xan shava	Sauna
6	Jìm	Yin maye	Jim
7	Kuràamaii	Mashaya shava	Kurame
8	Kwaskwaroo	Gidan shava	Kwaskwaro
9	Laakàsairàa	Shava a cikin roba	Suna ne na lemun kwalba

10	Lîish	Shalosho	---------
11	Mài àljànnuu	Xan shava	Mai iskoki
12	Màasu àljànnuu	Mashaya shava	Masu iskoki
13	Tsûmmaa	Abin naxe shava	Tsumma
14	‘Yan leedàa	‘Yan shalosho	Masu leda

Kalmomi masu xauke da Saye/ Qirqira

A kalma mai lamba 1 da 2 da 3 da 4 da 5 da 6 da 7 da 11 da 12 da 13 da kuma 14.

Kalmomi masu xauke da Fassara/ Aro

A kalma mai lamba ta 9 da 10.

‘Yan shava ba su da jimloli da suke sadarwa da su kasancewa ba surutu suke yi ba, wannan ya haifar da yanayi na sadarwa da a iyaka sanin mai bincike bai cikaro da jimloli ba da suke yi ba a lokacin sadarwa.

4.4.4 Hausar ‘Yan Qwaya.

Qwayoyi jam’i ne na kalmar qwaya da ke nufin qanqanen abu mai nau’in hatsi kamar gero ko wake ko dawa ko masara ko makamantansu. Wani magani da ake haxiya mai sa maye ko hana barci (Qamusun Hausa, 2006:293). Abubuwan da akan sha da manufar yin maye.

Qwaya na cikin rukunin abubuwan sa maye (NARCORTICS) da suka haxa da ofiyun (Opium) da mofin (Morphine) da kodin (Codeine da Heroin). Qwaya nau’i ne na magani da ake sha domin a yi maye ta hanyar karya dokar da aka shimfixa ta shan wannan magani da ma’aikatan lafiya suka sharxanta. Ke nan, qwayoyi ko qwaya nau’i ne na kayan shaye-shaye da ake sha da manufar yin maye ta hanyar wuce qa’idar da aka shimfixa a lokacin sha ko domin sha.

Hukumar NDLEA ta bayyana Qwaya da ma’ana kamar haka :

> *“Qwaya ita ce dukkanin wani abu da za a sha ko a haxiye ko a shaqa kuma dalilin haka ya kawo canjin yanayin jiki ta hanyar samun kuzari ko kuma ya kawo kasala ko ya haifar da canjin qwaqwalwa ko tunani“*.
> (Gidan Dabino 2012 :10)

Matasa maza da mata su ne sahun gaba wajen amfani da waxannan qwayoyi cikin su akwai masu ilimin boko da marasa shi da ma na addini a wasu lokuta. Akwai kwayoyi nau’i da yawa da ake sha domin a yi maye. ‘Yan siyasa kan rinqa ba ‘yan bangar siyasa na sha domin su cimma burinsu na siyasa. Wannan lamari babbar matsala ce ga al’umma domin matasa da damar gaske sun tsunduma cikin wannan harka, wasunsu sun haukace a sanadiyyar hakan.

Kasancewar ‘yan qwaya masu aikata laifi ta hanyar aikata abin da hukuma da ma al’ada ba su aminta a yi ba, ya tilasta su qirqirar wani karin harshen rukuni da suke amfani da shi don kawar da hankalin jami’an tsaro da ma sauran mutane da ba harkar su ce ba shan qwayoyi. Akwai kalmomi da jumloli da suke amfani da su da kan bayyana nau’o’in qwayoyin da sunayensu da halin da ake shiga idan an sha.

Misali:

Lamba	**Kalma**	**Ma’ana (A)**	**Ma’ana (B)**
1	Afsìs	Qwaya	Suna ne
2	Faràaree	Qwayoyi	Fararen abu
3	Farin maalàm	Farar qwaya	Malami fari
4	Kaashiin àljannii	Qwaya	Kashi na aljanni
5	Laambàa 5	Baliyun D5	Maganin sa barci
6	Mulkìi	Sunan kwaya	Sarauta
7	Roocài	Wata irin qwaya ce	Suna ne
8	‘Yan wàasaa	Qwayoyi	Masu wasa

Kalmomi masu xauke da Saye/ Qirqira

A kalma mai lamba ta 2 da 3 da 4 da 6 da kuma 8.

Kalmomi masu xauke da Fassara/ Aro.

A kalma mai lamba ta 1 da 5 da kuma 7.

Lamba	**Jimla**	**Ma'ana (A)**	**Ma'ana (B)**
9	À ji garau	Wata irin qwaya ce	Suna ne
10	Taa fashèe	Fara yin maye/ shiga maye	Fashewar wani abu

Akwai saye da qirqira a waxannan jimloli guda biyu.

4.4.5 Hausar ‘Yan Kodin (Syrup)

Kodin na cikin rukunin nakotik (NARCORTICS) da suka haxa da Opium da Morphine da Codeine da Heroin. Siruf suna ne na nau’i daga cikin nau’o’in kayan da ake sha a yi maye. Asalin wannan kayan shaye–shaye ya faro ne daga maganin tari da ake ba marasa lafiya, sai matasa maza da mata suka mai da shi abin sha a yi maye ko a ji silo ta hanyar wuce qa’idar shan maganin na tari. Ana shan kodin ta hanyar kurva ta baki.

Shan siruf ko kodin ya kasance wutar daji a yau, domin kuwa matasa maza da mata musamman ‘yan makarantun firamare da sakandare da na gaba da sakandare irin kwalejojin ilimi da jami’o’i na shan kodin kai harma ‘yan mata da matan aure kan kore. Haqiqa abin ba a cewa komai, sai wanda ya gani domin ya fi qarfin misaltawa, duk yadda ka ji in ba gani ka yi da idon ka ba za ka xauka kawai ana kambama wa ne.

‘Yan kodin rukuni ne na mashaya waxanda suka mayar da shan maganin tari a matsayin abin sha a yi maye, ta hanyar wuce qa’idar da aka shimfixa domin shan maganin. Wannan ya haifar da samar ko qirqirar wani nau’i na Hausa ko karin harshe da suke amfani da shi ta yadda sai xan hannu kawai kan fahimci abin da suke nufi. Shan kodin a yau, babbar annoba ce da matasa maza da mata suka tsunduma ciki, suke matuqar sha da manufar yin maye ko a ji *‘silo’* wato kamar yadda suke cewa. Hakan ya haifar da wasu kalmomi da ma jimloli da suka kevanta da abubuwan da suka jivanci shan kayan maye ta zumar kemis.

Misali:

Lamba	**Kalma**	**Ma'ana (A)**	**Ma'ana (B)**
1	Beenii	Benilin	----------
2	Hâi	Buguwa	----------
3	Ìnzoo	Sirob	-------
4	Kafsìi	Kafsil (cafsil)	Kafso
5	Koofìi	Koflin	-------
6	Kofmìi	Kofmis (cof mix)	---------
7	Lagèewaa	Buguwa	----------
8	Murfii-murfii	Haxa kuxi a sayi kodin	Murfin rufe wani abu
9	Na mânyaa	Kodin (codin)	----------
10	Na qanaanàn yâaraa	Asafectal (expectol)	----------

11	Noobìi	Nobilin	----------
12	Tòotoo	Totolin (tutolyn)	----------
13	Zumàr kemìs	Kodin	Daga Kalmar zuma aka samo
14	Koodì	Kodin (codin)	----------
15	Silôo (slow)	Shiga maye	----------

Kalmomi masu qirqira/ saye ko kinaya

A kalma mai lamba 3 da 7-10 da kuma 12-13.

Kalmomi masu Fassara/ Aro

A kalma mai lamba 1 da 2 da 4-6 da 11 da kuma 14-15.

Lamba	Jimla	Ma’ana (A)	Ma’ana (B)
16	Baabaa yà akà yi nèe?	Salon gaisuwa da tambaya.	--------
17	Taa fashèe	Fara maye ko sa maye	----------
18	Yàa dai mastàa	Mai sayar da kodin	----------
19	Inàa sô nà yi hâii	Ina so in sha in bugu.	--------

An yi qirqira a waxannan jimloli masu lamba 16 da 17 da 18 da kuma 19. Akawi kuma aro/ fassara a lamba 18 da 19 baya ga qirqira.

4.5 Naxewa

Wannan babi ya yi qoqarin bayyana ma'anar Hausar kan titi, tare da warware Hausar ta hanyar bayyana sigogin Hausar. An fiddo da yanayin Hausar da masu sana'o'i mabambanta suke yi da kan bayyana rukunin da mai magana ya fito. Wannan ne ya sa aka tsunduma wajen kawo Hausar kan titi na masu sana'o'i na haya da abubuwan hawa da suka qunshi 'yan bas da 'yan a-cava, wadda wasu rukunonin Hausawa suke yi da niyyar cimma burin sadarwa a tsakaninsu. Irin wannan Hausa ana yi ne ta hanyar voye ko saye wasu muhimman saqwanni. Ana faxaxa ma'ana ko tattare ma'ana wuri xaya da manufar kawar da hankalin ko tunanin waxanda ba a son su fahimci abin da ake nufi. Haka kuma an yi qoqarin bayyana da kuma warware Hausar masu sayar da sayen kayan maye ta hanyar bayyana abubuwan a mahangar kwararru a fagen hana sha da fataucin kayayyakin da suke sa maye. An kawo Hausar rukuni na masu shaye-shaye da suka haxa da Hausar 'yan giya da 'yan wiwi da 'yan shalosho ko shava da 'yan qwaya sai kuma siruf ko kodin. Wato zumar kemis.

An yi qoqarin bayyana sigogin Hausar ta hanyar bayyana zubi da tsarin jimlolin da kuma azuzuwan aikatau da ake samu a yanayin Hausar da kuma Hausar da ake samu a garin Kano da Zariya da kuma Sakkwato ta fuskar masu haya da babura ('yan a-cava) da kuma mashaya wiwi.

Babi na Biyar:

Kammalawa

5.1 Taqaitawa

An gudanar da wannan kundin bincike ne ta hanyar yin amfani da babi-babi xai-xai har guda biyar. Kamar yadda kowane bincike kan kasance, wannan kundin bincike ma ya xauki turbar da waxancan suka xauka. An fara binciken ne da gabatarwa sannan aka yi shimfixa dangane da yadda aikin zai kasance, an kuma bayyana dalilan bincike da manufar bincike da farfajiyar bincike da muhimmancin bincike da hasashen bincike da kuma hanyoyin da aka gudanar da bincike ta hanyar amfani da manyan hanyoyi na gudanar da bincike. An kawo farfajiyar bincike da matsalolin bincike da kuma ma'anar wasu kevavvun kalmomi sai kuma naxewa. Mai bincike ya karkata akalar bincike wajen ganin an yi waiwaye da kuma bitar ayyukan da suka gabata masu alaqa ta kusa da ma nesa da wannan aiki. Domin Hausawa na cewa "waiwaye adon tafiya", wannan ya haifar da waiwayen da kuma bitar ayyukan da suka gabata a kan Hausar rukuni sai kuma naxewa.

A babi na uku mai taken mutanen kan titi da sana'o'insu. Kamar yadda 'yan magana kan ce a san mutum a san cinikinsa, wannan ya haifar da yin bayani a kan karin harshe da majiya harshe xaya da kuma dangantakar harshe da al'umma. Sannan an kawo ma'anar kan titi da rayuwar kan titi da mutanen kan titi nagari da lalatattu da sana'o'in kan titi da suka haxa da masu motocin haya 'yan bas da 'yan tasi da kuma 'yan a-cava (masu haya da babura). To, tun da kuwa ana bincike ne a kan Hausar wasu mutane ya zama wajibi da a warware zare daga abawa. Hakan ya sa a babi na huxu a ka yi warwarar aikin ta hanyar fexe biri har wutsiya. An bayyana

sannan aka kawo ma'anar Hausar kan Titi da kuma Hausar 'yan haya da suka qunshi Hausar 'yan bas da Hausar 'yan a-cava. An yi bayani a kan sigogin Hausar kan titi a babi na huxu, Hausar masu sayar da sayen kayan sa maye da suka haxa da Hausar 'yan giya da 'yan wiwi da 'yan sholisho ko shava da 'yan qwaya da kuma 'yan kodin ko syrup da suke kira zumar kemist.

Yayin da a qarshe sai aka fara naxe tabarman binciken da taqaita abubuwan da aka duba a wannan bincike, sai bayanin iri abubuwan da bincike ya gano ya biyo baya. Daga nan kuma sai bayanin kammala bincike da shawarwari da ake ganin an samo su ne a dalilin wannan bincike.

A qarshen-qarshe aka kawo manazarta wadda ta kasance jagora wajen qarin bayani a kan wani ko waxansu bincike makamantar wannan.

5.2 Abubuwan Da Bincike Ya Gano

Sakamakon wannan bincike mai taken " Nazarin Hausar kan Titi" an gano abubuwa kamar haka:

I. Akwai alaqa ta qud-da-qud tsakanin harshe da zamantakewar mutum ko mutane ta fuskar sana'a wadda kan haifar da Hausar da wannan rukuni suke yi don sadarwa.

II. Harshen Hausa shakundum ne ta fuskar masu amfani da harshen domin kuwa kowane rukuni na Hausawa na da kalmomi da ma jimloli da suka kevanta da su kawai ta fuskar amfani.

III. Harshen Hausa na bunqasa sakamakon qirqira da aro da fassarar sababbin kalmomi da ma jimloli da ake samu, kuma ma'anarsu ta kevanta ne da wuri ko yanayin da ake ciki a lokacin sadarwar. Hausar kan titi ba wai Hausar mutanen banza ba ne ko ashararai ba.

IV. Amfani da irin wannan Hausa kan haifar da jawo hankalin mai sauraro da ma vad da hankalin mai sauraro ta yadda a wasu lokuta sai xan hannu kawai kan fahimci ma'anar da ake nufi ko wanda aka yi ma bayani.

V. Masu motocin haya musamman 'yan bas na amfani da kalmomi na musamman da suke sadarwa da su waxanda kan bayyana hali ko yanayi da suka tsinci kawunansu a lokacin gudanar da harkokin tuqin mota. Kamar yadda 'yan a-cava da mashaya kayan da ke sa maye kan yin Hausar da ta danganci ko ta kevanta ga sana'arsu da kuma abubuwan da kan sa maye da suke sha.

VI. Jimlolin da suke amfani da su a lokacin sadarwa sauqaqa ne domin zubi da tsarin mafi yawan su ba su da yankin suna sai yankin aiki kawai. Sannan ta vangaren azuzuwan kalmomin nahawu sun fi amfani da wakilin suna da aikatau da kuma bayanau, duk da yake akan sami sauran azuzuwan kalmomin Hausa na nahawu.

VII. Suna amfani da aikatau 'yan aji 1 da 2 da 4 da kuma aji 6.

5.3 Kammalawa

Bincike a kan nazarin Hausar kan Titi, babu shakka aiki ne mai ban sha'awa da nuna yadda harshen Hausa ya bunqasa ta fuskar masu amfani da harshen da ya danganci harkokin rayuwarsu da sana'o'i, da cigaban zamani. Kamar yadda Muhammad, (2011) ke cewa *"*Bayan masu sana'ar sadarwa ma, ai kusan kowace sana'a da ka sani a duniyar nan tana da irin tata gudummuwar da take iya bayarwa ga harshe, don kuwa ita ce take samar da irin Hausarta ta musamman wadda takan yaxu ta zama mallakar kowane mai amfani da harshen, sana'ar nan ta gargajiya ce kamar qira ko saqa ko dai ta zamani irin su kanikanci. Hasali ma dai, duk mai amfani da harshe yana da irin gudunmuwar da yake bayarwa wajen raya harshen, don kuwa ko kare ma da ranarsa".

Haka Wurma, (2002) ya yi magana a kan faxaxa ma'ana ko taqaita ma'ana, inda ya bayyana shi a matsayin wani fanni ne mai nuna cigaban harshe. Ga yadda ya bayyana lamarin: " A kusan kowace al'umma ana amfani da sababbin dabaru da kalmomi har da tunani domin tunqaran ci gaban zamani. Haka kuma a masu magana musamman matasa yanzu suna jin daxi wajen ba kalmomi sabuwar ma'ana, saboda su kauce wa tunanin masu sauraronsu" (Wurma, 2002:73).

Abin da ya gabata 'yar gudunmuwa ce dangane da yanayin amfani da harshen Hausa da aka kira Hausar kan titi da ke nuni da wani nau'i na Hausa. Akwai aro da qirqira da fassara da masu wannan Hausa suke yi da kan haifar da kinaya a kan abin da aka faxa. Wannan Hausa ba wai Hausar mutanen da ake wa kallon mutanen banza ko 'yan iska da zauna gari banza ne. A'a, a kusan kowane rukuni na masu sana'a a kan ci karo da ire-iren waxannan kalmomi da ma jimloli. Sauran maganar ita ce, amfani da harshen Hausa a kan titi al'amari ne da ya dogara ga mu'amala da yake aukuwa a tsakanin masu sadarwa da harshen Hausa. Hasali ma wannan mu'amula, ita take share fagen biyan buqatu da ka taso a sanadiyyar rarrabuwa tsakanin masu mu'amalar. Ita kanta mu'amala tana xarsuwa ne kan dangantakar cuxe-ni-in-cuxe-ka tsakanin mutane daban-daban wadda hakan ya yi dai-dai da dokar tsarin zamantakewa.

A irin wannan yanayi ne al'umma ko Hausawa da waxanda ba Hausawa ba suke amfani da harshen Hausa. Wannan ne ma ya sa aka kawo bayanin a kan ma'anar kan titi da mutanen kan titi da kuma sana'o'in da ake samu a kan titi, kasancewar sana'a ginshiqi wajen samar da Hausar masu ita. Duk da yake an yi amfani da Hausar kan titi ko kalmar titi ne a matsayin kinaya.

A san mutum a san cinikinsa. Idan kana qoqarin sanin wane ne wane, sai ka san yadda yake ta fuskar sana'arsa ko zamantakewarsa. Wannan ya sa aka yi tsokaci a kan 'yan bas da 'yan tasi da 'yan a-cava. Haka kuma akwai 'yan giya da 'yan wiwi da 'yan shava da 'yan qwaya da kuma 'yan kodin. Wani abin lura kuma shi ne cewa, mashaya a Kano da Zariya da ma Sakkwato na da kalmomi da ma jimloli da suka yi tarayya a fagen shaye-shaye da ma harkar a-cava ko kabu-kabu. Duk da yake akwai bambance-bambance a wasu wuraren ta fuskar qirqira ko aro da fassara na kalma da kan haifar da kinaya. Akwai kalmomi irin maye da buguwa.

5.4 Shawarwari

A sakamakon wannan bincike, waxansu shawarwari sun taso waxanda ake ganin idan an xauke su aka aiwatar za su haifar da xa mai ido. Waxannan shawarwari sun haxa da:

I. A cigaba da bincike mai alqa da harshe da walwalar harshe da zamantakewar al'umma don havaka harkan koyo da koyarwa a makarantu da cibiyoyin ilimi.

II. A halin da ake ciki a duniya, shirin game-duniya (Globalization) shi ne salon da duniya ko qasashen Turai suka amince da shi; kuma shi wannan tsari qoqari yake yi a kau da shingen da yake tsakani al'ummomin duniya ta fuskar tattalin arziki da siyasa da ma al'adu. Kawai duniya ta zama dunqulalliya a qoqarinsu na yaxa shiri ko aqidar jari-hujja. Cimma buri ko manufar wannan shiri na game-duniya ya ta'allaqa ne ta hanyar amfani da harshe, harshe ne ake yin farfaganda da shi kodai ta hanyar rubuce-rubuce a jaridu da mujallu da ma litattafai ko kuma ta hanyar kafofin yaxa labarai na wannan zamani, irin su intanet da talbijin da rediyo. To a sanadiyyar haka ya zama masu nazarin zamantakewar al'umma musamman na Hausawa da su kansu Hausawan su riqa duba irin wannan

bincike don su yi amfani da abin da suka koya wajen ganin an cigaba da yaxa harshen na Hausa da ma al'adun Hausawa. Kasancewar harshe na taka muhimmiyar rawa wajen isar da tunani da al'adun kowace al'umma.

III. Bahaushe dai kan ce, "da na gaba ake gane zurfin ruwa". Saboda haka, masu nazarin walwalar harshe da zamantakewar al'umma da jami'an hukumar hana sha da safarar miyagon qwayoyi da sauran jami'an tsaro da masu nazarin tattalin arziki da ma iyaye su karkato hankularsu zuwa ga nazarce-nazarcen ayyuka irin wannan wajen fasalta al'amurran da suka sa a gaba.

IV. Gwamnati ta kafa makarantu ko cibiyoyin nazari ko kuma aqalla sashen da yake koyar da nazarin walwalar harshe da zamantakewar xan-adam masu cin gashin kansu. Sannan a tallafe su da duk abubuwan da suka dace a yi amfani da su don tabbatar da an ilmantar da 'yan qasa da ma su kansu Hausawa.

V. 'Yan qasa kuwa, su shisshiga irin waxannan makarantu ko cibiyoyi idan an kakkafa su.

VI. Su kuma xaliban nazarin harshe da al'adu da nazarin zamantakewar xan-adam su taru su haxa gwiwa wadda zai qara musu zumunci. Domin Hausawa kan ce 'sabo da maza jari ne'.

VII. Hausawa su cigaba da adana al'adunsu da harshensu, domin kuwa waxannan abubuwa ba qashin yadawa ba ne. A saboda irin wannan yanayi na rayuwa da duniya take ciki, wato shirin game-duniya da tsarin jari-hujja.

VIII. Masu nazarin zamantakewar al'umma na iya nazartar harshe don havaka ko faxaxa faggen iliminsu.

IX. Hukumar hana sha da fataucin miyagun qwayoyi ta qasa na iya nazartar harshe don gano yadda masu aikata wannan xanyen aiki suke sadarwa da harshen Hausa a qoqarin rage da ma kawar da wannan harka.

X. Irin wannan bincike zai iya havaka harshe ta hannun masu sana'o'i da watau harkokin rayuwa mabambanta.

XI. Masu sharhin al'amuran yau da kullum na iya nazartar harshe a matsayin majingina wajen fasalta al'amurran yau da kullum na rayuwar Hausawa ta hanyar sadarwa.

MANAZARTA

Abdullahi, Y. A. (1934). ‘ The Roman Transliteration of Holy Qur’an’.

Abubakar, I.A. (2001). “Dangantakar Harshe Da Addini: Nazari A Kan Karin Hausar Gardawa A Birnin Kano Da Kewaye”. Takardar Da Aka Gabatar A Taron Qarawa Juna Ilimi Tsakanin Malamai da Xalibai. Kano: Jami’ar Bayaro. (unpublished)

Adamu, M. (1976). ‘The Hausa Factor in West African History ABU Press, Zaria, Wanda A. G. Wurma Ya Fassara da “Tasirin Hausawa a Tarihin Afirka ta Yamma” a matsayin kundin digirinsa na biyu. Zariya: Jami’ar Ahmadu Bello a 1991’.

Adamu, A.U. (2008). “Salon Taxin Mata Hausawa a cikin Garin Kano”. Kundin Digiri na Biyu. Kano; Jami’ar Bayero.

Adeyanju, T.K. (1989). “*Sociolinguistics and Language Education*: An African Perspective. Department of Education”. Zaria: Ahmadu Bello University.

Ahmed, A & Daura, B. (1970). “*An Introduction to Classical Hausa Major Dialects*”. Zaria: NNPC.

Almajir, T.S. (2010). “Zamantakewar Hausawa Matasa A Qarqashin Shirin Game-Duniya”. *Harshe 4. Journal of African Languages*. Department of Nigerian Languages. Zaria: Ahmadu Bello University.

Amfani, H.A. (2011). “Hausa Da Hausawa: Jiya Da Yau Da Gobe”. Muqalar da aka gabatar a Taron Qarawa Juna Ilimi. Zariya: Jami’ar Ahmadu Bello.

Amin, M.L. (2002). “The Hausa Metaphysical Worldview A Paremiological Exposition”. Ph.D Dissertation. Zaria: Ahmadu Bello University.

Andrew, E.I. (2010). “Language Variation in NAF Base Kaduna”. Department of English and Literary Studies. Zaria: Ahmadu Bello University.

Ashiru, A. (2000). “The Use of Slang in Kantin Kwari Market Kano”. Kundin Digiri na Biyu. Kano: Jami’ar Bayero.

Azare, Y.M. (2011). "Language in Diversity: A Look At the Role of Women Towards Language Development in Hausa Socio-Linguistics Setting". In Studies in Hausa Language, Literature and Culture. The 6th Hausa International Conference. CSNL Kano: Bayero University

Bargery, G.P (1993). "A Hausa-English Dictionary and English – Hausa Vocabulary". Zaria, A.B.U Press.

Babanzara, M. H. (2006). "A Typology of Hausa Jagon". In Fais: *Journal of Humanities* Vol. 3. No. 4, Kano: Jami'ar Bayero.

Bashir, M.S. (2004). "The Burnoan Hausa: A Pidgin or A Stripped Down Language". *In Algaita Journal of Current Research in Hausa* Vol. 2 No. 1.

Bayero, A. Y. (1997). *Jigon Nazarin Waqa*. Fisba: Kaduna

Bello, A. S. (2002). "Language and Identity: Reflecting on Language Politics in Nigeria". In Algaita Journal of Current Research in Hausa. Vol. 2, No. 1.

---------- (2012). Ci-Gaba da Nazari A Kan Karin Harshe Na Rukuni: Tsokaci A Kan Hausar 'Yan Shaye-Shaye. Muqalar da aka Gabatar a Taron Qarawa Juna Sani. Sashen Hausa. F.C.E: Zariya

Bendo – Samuel, J. and et al (1976). "A Provisional Language Map of Nigeria". In Savanna Journal of Environmental and Social Sciences. Vol. 5, No. 2. Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Bunza, A. M (2005). "Arashi Gogi Baqauye: Nazarin Karin Maganan Arashi Da Ke Jikin Motoci". Takardar Da Aka Gabatar A Taron Qara wa Juna Sani Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya. Sakkwato : Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Crane, L.B., Yeager, E. and Whitman (1981). *An Introduction to Linguistics*. New York: Holt Rinehart and Winsfon.

Crystal, D. (1980). *A Dictionary of Liguistics and Phonetics*. Sixth Edition. Blackwell Publishing.

Daba, H. A. (1997). "Linguistics Taboos and Animal Categories as Verbal abuse of Compliment in Hausa". In Harsunan Nijeriya. Vol. XVII. Kano: Jami'ar Bayero.

---------- (1987). "Sociolinguistic Study of Address Terms in Hausa". PhD Dissertation . Madison University Wisconsin.

Daura, M (1974). "*Harshen Hausa*" A paper presented during the activities of Hausa week. Kano: Abdullahi Bayero College.

Xantumbishi, M.A. (1987). "Dialect: A Case of Bourgeois Socio-Linguistic Phenomenon". A Paper Presented at the 4th International Conference on Language, Literature and Culture.

---------- (2003). "A Study Of Hausa Slang In Kano Metropolis: A Sociolinguistic Approach". PhD Dissertation. Department of Nigerian Languages. Sokoto: Usmanu Xanfodiyo University

---------- (2008). "Salon Sarrafa Harshe Da Karkasuwar Hausa Rukuni-Rukuni". In *Algaita Journal of Current Research in Hausa* Vol.1 No. 5.

---------- (2011). "The Development and Role of Hausa Slang in Northern Nigeria: A Socio-Linguistic Perspective". In Studies in Hausa Language, Literature and Culture. The 6th Hausa International Conference CSNL. Bayero University: Kano.

Dawakin Tofa, M. I. (2005). "Karin Harshen Mahauta". Kundin Digiri na Biyu. Kano: Jami'ar Bayero.

Fagge, U.U. (1982). Dialectal Influence in the Choice of Voiceless Labials in Kano Hausa. M.A Dissertation. Kano: Bayero University.

---------- (1999). "Tasirin Karin Harshe na Rukuni wajen Qirqirar Sababbin Ma'anoni a Hausa". Takardar Da Ya Gabatar A Taron Qarawa Juna Ilimi. Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero

---------- (2002). "Zaurance Zawarawa a Birnin Kano da Kewaye". In *Algaita Journal of Current Research in Hausa.* Vol. 2 No. 1.

---------- (2004). *Ire-Iren Karin Harshen Hausa na Rukuni.* Benchmark Publishers Limited: Kano.

Fasold, R. (1990). *Socio-Linguistics of Language.* U.S.A: Blackwell.

Fromkin, V. and Rodman, R. (1978). *An Introduction to Language*. 2nd Ed. New York, Holt, Rinehart and Winston.

Galadanci M. K (1980). *A Text Book Of Methodology:* Zaria.NNPC.

Gidan Dabino, A. A (2012). *Mata Da Shaye-Shayen Kayan Maye: Ina Mafita*? Kano Nijeriya. Gidan Dabino Publishers.

Gumbers, J. and Hymes, D (1972). *Direction in Socio-Linguistic*. Reneheart and Wington.

Hornby, A. S (2000). Oxford Advanced Learners Dictionary. Oxford: University Press.

Hudson, R.A. (1980). *Socio-Linguistics*. London: Cup.

Hymes, D (1964). *Language In Culture and Society*. New York. E. E. Evans Pritchard Publishers.

Jaggar, P. J. (2001). Hausa. Amserdam. John Benjamins Publishing Company.

Jibrin, S. (2006). "Kwatanta Hausar Mutanen Eggon Da DaiDaitacciyar Hausa". Kundin Digiri na Biyu. Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Kabir, B. U. (2004). "Nazari A kan Hausar Mata Matasa a Cikin Garin Kano". Kundin Digiri na Biyu. Kano: Jami'ar Bayero.

Kirk-Greene, A. H. M. (1973). "Mutumin Kirki' (The concept of the Good Man in Hausa). The Third Annual Hans Wolff Memorial Lecture. Bloomington, Indiana: Indiana University.

Qamusun Hausa (2006). Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Kano: Jami'ar Bayero.

Lado; R. (1964). *Language Teaching*. A Scientific Approach. New York: MacGraw-Hill.

Lawal, H. S. (2011). "Faxaxa Ma'anar Kalmomi Da Jumloli A Hausa". Kundin Digiri Na Biyu. Sashin Nazarin Harsuna Da Al'adun Afirka: Zariya. Jami'ar Ahmadu Bello.

Lyons, J. (1970). *Semantics.* Vol 2. London: Cambridge University Press.

Muhammad, X. (1990). *Hausa Meta-Language*. Vol. I (Kamus Na Kevavvun Kalmomi). Ibadan: University Press Limited.

---------- (1997). "Nagari Na Kowa: Nazarin Tunanin Hausawa Da Adabinsu". Laccar Tunawa Da Marigari Farfesa Ibrahim Yaro Yahaya.(1944-1995). Kano Nijeriya: Jami'ar Bayero.

---------- (2006). "Tsakanin Hamada Da Hamdala: Waiwayen Gudunmuwar Jami'o'i, Ga Havaka Harshen Hausa". In *Algaita Journal of Current Research in Hausa Vol. 5. No. 1*.

---------- (2011). "Hausa A Duniyar Yau: Tasirin Shirin Game-Duniya Kan Harshen Hausa". In Studies in Hausa Language, Literature and Culture. The 6th Hausa Internatinal Conference. CSNL Kano: Bayero University.

Muhammed, A. I. (2011). "Hausar Kwantagora: Nau'o'inta Da Sigoginta". Kundinn Digiri Na Biyu. Sashen Nazarin Harsuna Da Al'adun Afirka: Zaria. Jami'ar Ahmadu Bello.

Muntari, H. (2008). "Karin Harshe Na Rukuni A Hausa: Nazari A Qasar Zazzau". Kundin Digiri na Biyu. Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Musa, A. (2011). "Hausa-Niga: Nazari A kan Walwalar Harshe da Zamantakewa Tsakanin Rukunin Matasa Maza Hausawa a Yau". In *Studies in Hausa Language, Literature and Culture. The 6th Hausa International Conference.* CSNL. Kano: Bayero University.

N.D.L.E.A (2004) Drug Abuse Awareness Guide. Drug Demand Reduction Directorate, National Drug Law Enforcement Agency. Ikoyi: Shehim Ventures Limited.

Osisanwo, W. (2003). Introduction to Discouse Analysis and Progmatics. Lagos: Femolus Fetop.

Peter, T. (1974). *Socio-Linguistics: An Introduction to Language and Society*.

Romaine, S. (1994). *Language in Society: An Introduction to Socio-Linguistics.* Oxford: University Press.

Rufa'i, A. (1986). "Dangantakar Harshe da Al'umma" Paper presented at Hausa Week, School of Preliminary Studies. Kano: Jami'ar Bayero

Sapir, E. (1956). Culture Language and Personality. Berkeley: University of California Press.

Skinner, N. (1968) The Origin of the Name Hausa. *Africa Volume 38:Pp 253-257.*

Sani, M. A. Z. (2001). *Alfiyyar Mu'azu Sani 3. Karorin Harshen Hausa A Waqe*. Kano: Benchmark Publishers Limited.

Trudgill, P. (1974). *The Social Differentiation of English in Norwich.* Cambridge: University Press.

---------- (1983). *Socio-Linguistics 2nd* Edition. Harmonds Worth Penguin Books.

---------- (2000). *Socio-Linguistics: An introduction to Language and Society.* 4nd Edition. Harmonds Worth Penguin Books.

Umar, A.W. (1990). "Hausa Kingship Terms: A Problem in Universal Semantics". MA Thesis. Kano: Bayero University.

Wales, K. (1989). *A Dictionary of Stylistics*. London: Longman

Wardhaugh, R. (1988) *An Introduction to Socio-Linguistics.* London: Basil Blackwell.

Wurma, A.G. (1998). "A Synchronic Study of Linguistic Changes in Hausa". PhD Dissertation. Zaria: Ahmadu Bello University.

---------- (2002). "Semantic Changes Occuring in Hausa Language". *In Algaita Jounal of Current Research in Hausa* Vol. 2. No. 1.

Yakasai, S. A. (2002). "Socio-Linguistic Factors in Nigeria-Niger Border: Some Phonological Differences and Adaptation". In *Studies in Hausa Language, Literature and Culture.* The 5th Hausa International Conference. CSNL Kano: Bayero University.

---------- (2003). "Sadarwa Tsakanin Maza Da Mata: Nazarin Dangantakar Harshe Da Daidaituwar Jinsi". Muqalar da aka gabatar a taron qara wa juna ilimi. Sakkwato: Jami'ar Usman Xanfodiyo.

---------- (2010). "Tasirin Zamanantar Da Duniya Cikin Nazarin Harshe A Nijeriya". In *Xunxaye Jounal Of Hausa Studies.* Vol.1, No 3. Dept. Of Nigerian Languages. Sokoto: Usmanu Xanfodiyo University.

---------- (2012). *Jagorar Ilimin Walwalar Harshe*. Sokoto: Garkuwa Media Services LTD.

Yakasai, M. G. (2004). "Yanayin Karin Harshen Sojoji A Barikoki: Nazari A kan Barikokin Bukavu da na Jan-Guza". Kundin Digiri na Biyu. Kano: Jami'ar Bayero.

---------- (2011). "Yanayin Karin Harshen Sojojin Barikin Bukabu". In *Studies in Hausa Language, Literature and Culture.* The 6th Hausa International Conference. CSNL. Kano: Bayero University.

Yahaya, I. Y (1992). *Darussan Hausa*. Don Manyan Makarantun Sakandare. Littafi na 3. Ibadan: University Press Limited.

Zarruq, R. M. da Al-Hassan . (1986). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa* Don Qananan Makarantun Sakandare. Littafi na I da na II. Ibadan: University Press Limited.

Zarruq, R. M, da Al-Hassan, B.S.Y da Adamu, A. K. (1990) Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa.

Zarruq, R.M. (2001). "Nazarin Karin Harshe Na Hausa". Manuscript.

Hira Da Tattaunawa.

Popoola, F.A. (12-11-2011). Jami'ar Hukumar NDLEA. Zariya: Gwargwaje.

Muhammadu, T. (20-10-2011). Direba mai tuqin motar haya ta bas. Zariya

Uwaisu, D. (5-10-2012). Direba mai tuqin motar haya ta bas : Zariya

Sanusi, A. (Rafson) 3-7-2012. Tattaunawa da shi

Almu, Getso (2-2- 2013) Tattaunawa da shi a Sakkwato